# HARSHEN FARANSANCI A DUNIYA

## Tsarinsa na 2022



**Kashi na 2022**

Gallimard | Organisation internationale de la Francophonie

# ƘUNSHIYA

Shimfida 3

Gabatarwa 4

## SASHE NA 1

### Kasancewa da kuma amfani da harshen Faransanci a Duniya

- Yawa da kuma rabe- raben ƙasashen da ake magana da Faransanci a duniya. 6
- Hangen Faransanci ta cibiyoyin sarrafawa masu yawa 10
- Harshen Faransanci da amfani da harsuna masu yawa a manyan ƙungiyoyi na duniya 13

## SASHE NA 2

### Manufofin harshe da koyarwa da harshen Faransanci da kuma koyar da Faransanci a duniya

- Faransanci a matsayin harshen koyarwa 20
- Faransaci a matsayin harshen ƙasar waje 21

## SASHE NA 3

### Harshen Faransanci da al'ada a yanar gizo

- Matsayin Harshen Faransanci a yanar gizo 26
- Al'adun mutane masu magana da harshen Faransanci da ke zube a yanar gizo: Abubawan da suka shafe su da kuma matsalolinsu 28
- Littafin da kuma mawallafan harshen Faransanci 31

# SHIMFIƊA



Wannan rahoto da ke biye ba wani bayani ne game da harshen Faransanci ba, gabatarwa ne, bayani na kamar a idonka aka yi na yunkurin masu magana da Faransanci a duniya baki ɗaya. An fara ne da wannan hasashe: An haife mu ne a ƙalilan da al'adar Faransanci ƙalilan: "kuma muka kasance mun bunkasa ta kowane ɓangare".

Wannan shiri na samar da hadin kai tsakanin ƙasashe masu magana da harshen Faransanci kamar yadda yake a cikin wannan rahoton ya ci gaba ne da zama kashi kashi, ko kuma ma mu ce abu da yana sarrafuwa ta cibiyoyi masu yawan gaske. A takaice ana iya cewa tunbin giwa.


Shirin samar da hadin kai tsakanin ƙasashe masu magana da harshen Faransanci na bunkasa ne saboda shi ne abu ɗaya tilo mai karfin da zai iya haifar da haka ga mabambanta al'umma da ke yankin Afrika kuma a kan matasanta. Harshen Faransanci na ci gaba da bunkasa da kasancewa harshen mutanen Afrika, a makarantu, a rubuce-rubucensu da harkokinsu na gudanar da bincike da kuma tunaninsu. Wannan harshe yana ci gaba da mamaye tituna da kasuwanni da birane da a kullum suke ci gaba da kafuwa.

Wannan shiri na samar da hadin kai tsakanin ƙasashe masu magana da harshen Faransanci na ci gaba ne saboda ba ya ƙyamar kowa, kowa nasa ne a koyaushe. Kashe-kashe da rabe-rabe da ke ci gaba da faruwa a cikin al'umma masu mabambantan al'adu ya sa suka mayar da hankalinsu ga harshen da shi ne ya haɗa su. Muna iya cewa wannan shiri ne da za a iya kallonsa ta hanyar wata tsohuwar magana da ke cewa cibiyarta na nan a ko'ina kuma ba shi da gefe a ko'ina.

Kasancewar wannan shiri na samar da hadin kai tsakanin al'umma masu magana da harshen Faransanci shiri da ya shafi al'umma masu al'adu mabambanta da sashe daban daban na duniya, sai ya kasance tamkar wani abu ne da ya haɗe duniyar baki ɗaya duk kuwa da kasancewarta kashi kashi. Manufa a nan ita ce kasancewar duniya kashi kashi abu ne tabbatacce, amma kuma wani abu na tinkaho da ke bukatar wayewar kai. Wannan shiri wata hanya ce da ke ƙara tabbatar da cewa lalle a cikin duniya akwai harsuna daban daban, kuma hakan abu ne mai kyau a ko'ina. Abu na farko da hakan ya haifar shi ne tunani daga wani harshe zuwa wani, wanda haka zai hana zaman gidadanci, sai sa a sami wayewar kai da fahintar juna.

A dalilin haka ne wannan rahoto ya dage a kan nuna hatsarin dogaro da harshe ɗaya a cibiyoyi da kuma hulɗa a duniya. Ba magana ce ta tilasta wa al'umma wani harshe babba, mafi karɓuwa ba, kawai so ake a fahinta cewa a wannan duniya mai tattare da al'adu da tabi'u iri-iri, wanda hakan ke nuni da cewa al'umma a wani lokaci dole za a so a fahinci juna fa fuskar magana da harshe. Hirarrakinsu wanda ka iya kasancewa da wahala, da huldarsu, wanda wani lokaci ana iya samun rashin fahimta. Abin da yake gamagari wanda kuma ya kamata mu yi nasara a kansa tare, shi ne kamar yadda wani masanin falsafa mai suna Maurice Marleau-Ponty, kasancewar "abu a tsaye" ko "a gicciye" ya fi a ce an gan shi "a rataye".

Mafita a wannan duniya mai cike da harsuna iri-iri da al'adu mabambanta ɗaya ce, wato shirin samar da hadin kai tsakanin ƙasashe masu magana da harshen Faransanci.



Souleymane Bachir Diagne
*Jami'ar Columbia*

# GABATARWA

Wannan kashi na 5 na Harshen Faransanci a faɗin duniya ya kai mu ga tsakiyar mabambantan wannan shiri na samar da haɗin kai tsakanin ƙasashe masu magana da harshen Faransanci waɗanda aka same su, kuma a rainonsu ta hanyar balaguron harshen Faransanci na tsawon shekaru masu yawa. Da yawan masu magana da harshen da suka kai yawan mutane miliyan 321, harshen Faransanci har yanzu shi ne na biyar a cikin harsunan da aka fi yin magana da su a duniya. Wadanda suke gabansa su ne harshen Ingilishi da Sinanci da Hindu da Isfaniyanci.

Aikin da aka yi ta hanyar nazarin bincike da aka gudanar a jami'o'i da kundaye da aka tanadar da sauran hanyoyin adana bayanai a kan yadda harsuna suke yaɗuwa a cikin al'umma, da tattaunawa da shaida, yana bayani ne a kan yadda ake amfani da harshen Faransanci, da ire-ire bambance-bambance nan da ake samu ta hanyar amfani da harshen cikin al'umma.

Aikin ya taɓo wani abu da ba ƙasafai ake samu a rubuce ba cewa mafi yawa daga masu magana da harshen Faransanci da ƙananan yara da ke zaune a nahiyar Afrika an koyar da su ne da harshen Faransanci a makarantun da suka yi.

Domin fahintar aikin sosai an gayyace mu wajen yawo gani da ido a « Duniyar ƙasashe Rainon Faransa » a farkon aikin. A nan ne aka buɗe mana adadi da rabe-raben mutane masu magana da harshen Faransanci a faɗin duniya. Aikin ya nuna mana gaskiyar masu magana da harshen da kuma yadda suka mallake shi, da yadda aka yi masa wasu 'yan canje-canje da kuma ƙare-ƙare da masu magana da harshen ke yi masa da dai sauran abubuwa da suka shafi haka. Gabatar da sakamakon nazari da aka ɗauki tsawon shekara guda ana yi cikin ƙasashe a ƙalla goma sha biyu a Afrika da kogin Indiya ya ba mu damar tinkarar ire-iren harshen Faransanci sosai kuma ba tare da wasu matsaloli ba.

Daya daga cikin abubuwa da dama da suka shafi halayyar harshen Faransanci da kuma bambance-bambancen da ake samu wajen amfani da shi, ya sa muka yanke shawarar wani abu da ya shafi yin amfani da harsuna da yawa ƙungiyoyin duniya. Mun yanke shawarar mu dubi tasirin shirin nan mai taken « sa ido, da ɗaukar mataki nan take » da aka fara yinsa a shekarar 2020. Wanda ya gabatar da wannan shiri shi ne Babban Sakataren shirin samar da haɗin kai tsakanin ƙasashe masu magana da harshen Faransanci Mrs Louise Mushikiwabo wadda a cikin tattaunawar da muka yi da ita ta ce mana, « yin amfani da harshe mai yawa wani abu ne muhimmi na haɓaka dangantaka tsakanin ƙasashe, yana da kyau kuma abu ne da ya cancanta a kare shi ».

Sashe na biyu na littafin ya kasance ne cike da bayanai gane da yadda ake koyon Faransanci da kuma yadda ake koyarwa cikin harshen Faransanci a cikin shekaru fiye da 160. Nazarin canje-canje da ake samu a duniya da ci gaban da ake samu da kuma matsalolin da ake fuskanta, sakamakon nazari da aka samu a kowane sashe cike yake da bayanai cikakku na ginshiƙan abubuwa da suke da tagomashi a harkar yin amfani da harsuna da yawa a sashen ilmi. Kuma dama ce ta yin dubi zuwa ga harkoki iri-iri da shirin samar da haɗin kai tsakanin ƙasashe masu Magana da harshen Faransanci ke ba da tallafi a kai domin samun nasarar fiye da **ɗalibai miliyan 93** da Faransanci yake masu a matsayin harshen koyarwa a makarantu

A matsayin harshen ƙasar waje, Faransanci shi ne harshe na biyu da aka fi koyo a duniya da mutane fiye da **miliyan 50.** Idan aka yi nazarin yadda ake amfani da harshen Faransanci wajen koyarwa, za a ga abu ne yiwuwa harshen ya wuce matsayin harshen da ake amfani da shi kawai wajen koyarwa ko harshen 'yan boko, ya zama harshen da za a iya amfani da shi wajen samun aiki ko na ci gaban ɗalibai daga wani mataki zuwa mataki na gaba. Za kuma mu ga bukatar da ake da shi na harshen Faransanci yana da muhimmanci kuma yawan masu koyon harshen ƙaruwa yake yi sosai a wasu sassa na duniya (Afrika da Amurka da Asiya) ko da kuwa koma bayan da ake gani a ƙasashen Turai ya kai ga tsayawarsa cik a duniya.

Sashe na uku ya fara ne da samar da bayani na kasancewar harshen Faransanci a yanar gizo, ya tabbatar da cewa harshen **shi ne na huɗu** (bayan Ingilishi da Isfaniyanci da Larabci). Ya kawo shawarar hanyar da za a bi wajen samar da hanyoyin amfani da harshe bai ɗaya a duniyar yanar gizo, wanda ya nuna yadda harshen Faransanci da Ingilisha suka tsere wa sauran harsuna.

Daga ƙarshe sai bayanin halin da ake ciki a kan tambayar nan ta gano abubuwa da suka shafi al'adu wanda ya tabbatar mana da muhimmancin walafa shirrye shirye ta hanyar zamani da suka shafi ji da gani da kaɗe-kaɗe musamman idan akwai bukatar haka. Ko kuma a kawo bayani na taron duniya na farko da aka gudanar na marubuta masu magana da harshen Faransanci da kuma halin da littafan harshen Faransanci ke ciki a duniya. Za mu iya tunawa da yadda littafai suke a ƙasar Faransa da kuma yadda karatu ya nuna yadda tarin al'adu da kuma matsalolin da ya kamata a yi gyara a kansu.

Alexandre Wolff
*Shugaban Sashen Kulawa*
*da Harshen Faransanci*



SASHE NA 1

# KASANCEWA DA KUMA AMFANI DA HARSHEN FARANSANCI A DUNIYA

Karuwar mutane masu magana da harshen Faransanci a nahiyar Afrika ci gaba yake tsawon shekaru da dama. Rabe-raben masu magana da harshen faransanci ya ɗan sami kwaskwarima tamkar yadda amfani da wannan harshen ya canza musamman a ya yin amfani da shi cikin al'umma masu harsuna da yawa irin nahiyar Afrika. Hanyoyin koyon harshen Faransanci ya haɗa da hanyar da za mu kira ta gargajiya, wato ta koyo (amma ba ita kaɗai ba ce). Ana amfani da harshen Faransanci sosai ko kuma akasin haka, ya dai danganta da ƙasar da abin ya shafa. Akan haɗa shi da wani ko ma wasu harsunan a harkokin irin na rayuwa, misali kamar a wajen makaranta ko a wajen ofis. Daɗin daɗawa su waɗannan sabbin masu amfani da harshen waɗanda akasari Faransanci ba shi ne harshensu na haihuwa ba, sukan kasance sun haɗa shi da ƙwarewarsu na wani harshen. Wannan na kara yanayi da harshen Faransanci zai yi hulɗa da wasu harsuna na gida wanda kuma hakan kan haifar da ƙirƙira na kalmomi da haɗin jimla ko cikin maganganu na yau da kullum. Hakan kuma a kan sami wasu abubuwa daga wasu harsuna, wanda daga ƙarshe sai ya haifar da wani abu da ba karɓaɓɓen Faransanci ba, kamar yadda Darakta na ODSEF[1] ya ce, " An haife mu da Faransanci ƙalilan kuma a hankali muka bunƙasa."

## YAWA DA KUMA RABE-RABEN KASASHEN DA AKE MAGANA DA HARSHEN FARANSANCI A DUNIYA


A shekarar 2022, an ƙiyasta akwai **masu magana da harshen Faransanci miliyan 321**[2] a duniya. Faransanci ya ci gaba da riƙe matsayin na biyar cikin harsunan da ake yin magana da su a duniya bayan Ingilishi da Sinanci da Indiyanci da Isfaniyanci[3]. A cikin shekaru huɗu kacal, an sami ƙarin mutane miliyan 21 masu magana da Faransanci. Wannan ya nuna an sami ƙarin kaso kashi bakwai cikin ɗari daga shekarar 2018. Wannan bunƙasa da harshen ke yi tun shekaru da dama na ci gaba duk da kuwa an sami wani ɗan tsaiko a wani lokaci. A dai wannan wuri an sami ƙarin mutane masu magana da Faransanci da kusan kashi goma cikin ɗari tsakanin shekara ta 2014 zuwa 2018.

[1] Observatoire démographique et statistique de l'espace francophone de l'Université Laval à Québec.

[2] Don cikakkun bayanai na lissafin, duba bayanin binciken Richard MARCOUX, Laurent RICHARD da Alexandre WOLFF. Estimation des populations francophones dans le monde en 2022. Sources et démarches méthodologiques. Québec, 2022, Observatoire démographique et statistique de l'espace francophone (ODSEF) Université Laval. Duba qrcode.

[3] kimanta yawan masu magana da harsunan sun fito ne daga aikin Ethnologue, Languages of the World. 23e édition, 2020 a fadin Wikipédia.

Kamar yadda masu karatu suka saba karantawa, maganar ya haɗa da hanyoyi iri daban-daban da harshen Faransanci ke bunƙasa. Domin samar da tsari mai kyau da nagarta mun zaɓi mu bambanta tsakanin haɗin kan masu magana da harshen Faransanci *na yau da kullum* a duniya a haife shi cikin Faransanci kuma ya rayu. Wato daga wuraren da Faransanci yake a matsayin harshen waje (Graph Duniyar ƙasashe Rainon Faransa a 2022). Kasashe 36[4] da abin ya shafa tare da kasancewar suna da kashi 80 na masu magana da harshen Faransanci na duniya, su ne zakaran gwajin dafi na rayuwa da makomar harshen Faransanci. Tabbas muhimmanci ginshiƙan koyon harshen Faransanci a matsayin harshen waje ba shi da wata makusa kuma yana nuni da yadda harshen yake ci gaba da zama abin sha'awa kuma mai amfani a duniyar da yin amfani da harsuna da yawa kullum ƙara bunƙasa yake yi. Duk da haka kamar yadda lissafi da sakamakon nazarce nazarce da muke tarawa fiye da shekara goma, a nahiyar Afrika ce makomar harshen Faransanci ke cikin mawuyacin hali.





A gaskiya, ba wai kawai bunƙasar yawan mutane masu magana da harshen Faransanci "Wanda aka haifa a ciki kuma ya taso a ciki ko kuma wanda kawai ya taso a cikin harshen Faransanci" ya kasance ya ɗan gota adadin da ake da shi a rubuce a duniya da ɗigo (+1[5]). Duka duka dai za a iya cewa yana wakiltar kashi 95 na ƙarin da aka lura yana faruwa.

[4] Algeriya, Andorre, Belgium (ciki har da fédération Wallonie-Bruxelles), Bénin, Burkina Faso, Burundi, Kamaru, Kanada (ciki har da Kanada-Nouveau-Brunswick, Kanada-Ontario et Kanada-Québec), Comores, Kongo, Kongo (Jamhuriyar Demokradiyya), Côte d'Ivoire, Djibouti, Faransa (da yankunanta na ketare), Gabon, Guinea, Equatorial Guinea, Haïti, Labanon, Luxembourg, Madagascar, Mali, Moroko, Mauritius, Mauritanie, Monaco, Niger, Jamhuriyar CentraL Africa, Rwanda, Senegal, Seychelles, Switzerland, Chad, Togo, Tunisiya, Vanuatu


[5] Wannan a zahiri ya ɗan fi ƙarfi, amma (iddan aka kwatanta da shekara 2018) sake fasalin ƙasa na jimlar yawan wasu yankuna inda masu magana da Faransanci ke yin nauyi fiye da 80% (Tarayyar Wallonie-Bruxelles, Guadeloupe, Martinique, Faransa Polynesia da Wallis da Futuna) da lissafi ya rage shi.

Fiye da mutane miliyan 19 cikin sabbin masu magana da harshen Faransanci da ke zaune a duniya akasarinsu 'yan Afrika ne.




Samun ƙarin kaso 2.5 sama da yadda aka samu a 2018, nahiyar Afrika ta tabbatar da cewa matsayinta babba ne a ci gaban masu magana da harshen Faransanci kuma hakan ya sa ta bambanta da sauran nahiyoyi.

Idan muka yi wa abin da muka gano kwaskwarima kaɗan, za mu iya ganin cewa wannan nagarta ya samu ne musamman saboda ƙasashen da ke yanki Afrika Kudu da Sahara wanda su kaɗai suna wakiltar sama da kashi 80 na bunƙasar ƙasashe masu magana da harshe a wannan wurin. A waɗannan ƙasashen, idan ka cire kaɗan, bunƙasar ya yi sama sosai, ya zarce na wasu. Baya ga adadin masu magana da harshen Faransanci na yau da kullum ya ƙaru da kashi 8 cikin ɗari tsakanin 2018 zuwa 2022 a ɗaukacin yankin Afrika Kudu da Sahara. –Tekun Indiya (SSA-IO).




A cikin wannan nagartaccen ci gaba da ake samu, yana da muhimmanci a yi nuni zuwa ga abubuwa guda biyu. Da farko dai ya kamata a sani ci gaban ƙasa yake yi a ko'ina ƙasa da abin da ya faru a shekarar 2014 zuwa 2018 kuma hakan ya ɓoye bambancin da ake samu tsakanin ƙasashe.

### Jinkirin Haɓaka?

Idan aka yi la'akari da ƙasashe, abu na farko da ya kamata a tuna shi ne, ba tare da kulawa da batun da za mu gabatar a ƙasa ba, haɓakar adadin masu magana da harshen Faransanci ƙasashen Afrika Kudu da Sahara da yankin tekun Indiya a koyaushe adadinsu daidai yake da adadin al'ummar a daidai wannan lokaci.


Duk da haka idan muka dubi ra'ayin duniya, za mu iya ganin cewa duka nahiyoyin duniya mutanen da aka haifa kuma suka tashi cikin Faransanci da kuma waɗanda suka tashi a Faransa shi ne farko na haɓakar adadin masu magana da Faransanci. Haɓakar dai har yanzu ba ya da ƙarfi kamar yadda bincikenmu na daya yake. Bambancin shi ne kaso 1 a Turai da Tsibiran Tekun Pacific, kaso 2 a Amurka da ƙasashen Afrika Kudu da Sahara da Tekun India, amma kuma kashi 10 a Afrika ta Arewa da Gabas ta Tsakiya.


Wata manuniya da ba dole ba ne a ce daidai ne da ta shafi lissafin da muke yi kowace shekara huɗu, ko shakka babu, ya fi muhimmanci idan za ka ɗan ja baya ka kalli abin na wani lokaci mai tsawo. Za a ga abin da za a samu a matsayin canji na kason al'umma da za a kira masu magana da harshen Faransanci[6] a kowace ƙasa a duniya "a haife ka ka tashi a Faransa ko ka tashi a Faransa".

Ba wata ƙasa a Kasashen Afirika da ta ga muhimman canje-canje na yawan adadin mutane masu magana da harshen Faransanci in aka kwatanta da adadin mutanenta. Tun shekarar 2020 ƙasashen da ake samu a cikin rukuni, su ne dai. Ana samun ƙasa da kashi hamsin idan ka cire ƙasashe biyar zuwa shida wanda su dama tuni sun wuce wannan shingen ko kuma suna kusa da wucewa. Za mu iya gani kamar alamar da ke fito mana mai rauni ne, wanda ke karya ƙarfin guiwa ƙasa da hasashen samun haɓaka mai girma da abokan hulɗarmu na Jami'ar Laval suka yi a cikin (Sauyin rayuwa da sa'idon bin diddigi na duniyar masu magana da harshen Faransanci ODSEF).

[6] Anan kuma zai zama haɗari a gabatar da canjin kashi ta ƙasa, tsakanin, misali, 2010 da 2022, ba tare da ninka faɗakarwa game da sauye-sauyen da aka yi a kafofin da aka yi amfani da su ba da kuma dogon bayani na fasaha na tasirin tsarin alƙaluma. Don haka mun zaɓi wannan hangen nesan.

# YAWAN QASASHE MASU MAGANA DA HARSHEN FARANSANCI A DUNIYA A SHEKARAR 2022






Mun sani cewa bambanci mai rauni ba dole ba ne ya ƙasance ya samar da amsa gamsasshe, amma duk da haka muna iya gabatar da shawara ta bai ɗaya.

Da farko ma kuma kowane irin matakin kariya muka yi amfani da shi, abu ne mai wuya mu yanke magana kai tsaye cewa akwai tushe mai ƙarfi na son ko kishin Faransanci a waɗannan ƙasashe. Harshen Faransanci dai yana nan, amma dai ba ya tagaza komai wajen ci gaba da riƙe matsayinsa nai na farko. Idan a lokaci mai tsawo, ƙasashe masu kishin Faransanci na ƙara haɓaka ne, to ya kamata mu fahinta cewa akwai alamu da ke nuna cewa a cikin shekaru ashirin ya yi karo da katanga. Ya faro daga ƙasa, domin idan za a iya tunawa, zamanin mulkin mallaka bai ba da wani agaji na a zo a gani ba wajen yaɗa harshen Faransanci cikin al'umma. An sami yaɗuwar harshen Faransanci ne a dalilin makaranta. Da taimakon ilmi, ya ci gaba da haɓaka amma dai a hankali. Wannan ya tabbatar da gargaɗin da muka yi ta yi tun a shekarar 2010 dangane da matakan da ya kamata a ɗauka idan ana so harshen Faransanci ya ci gaba da rayuwa a nahiyar Afirka.

**Daga ƙarshe dai**, ya tabbata cewa ƙalubalen da aka gabatar dangane da batun ingantaccen ilmi a harshen Faransanci ya zama wajibi a gabatar da su da gaggawa. Dangane da haka, sakamako na baya da aka samu a nazarce-nazarce na PASEC[7] wanda ya shafi ƙasashe goma sha huɗu (14)[8] da suka halarci taron ƙara wa juna sani na Ministocin Ilmi na ƙasashe Raino Faransa (CONFEMEN) babu wani ƙarfin guiwa da aka samu daga gare shi. A takaice ma an ƙiyasta cewa a farkon shirin[9], fiye da kashi hamsin da biyar cikin ɗari (55%) na ɗalibai ba su iya kaiwa gacin da za a iya cewa madalla ba a harshen. Haka kuma, bayan kammala makaranta, fiye da rabin ɗalibai ba su kai matakin yabo ba a wajen iya karatu. Rahoton PASEC2019 ya nuna sakamakon da ake samu sun fi na shekarar 2014 kyau duk kuwa da yake wasu ƙasashen ba su ci gaba, wasu kuma na komawa baya.


Abin da yake a bayyane a nazarin halayyar al'umma shi ne wasu halayya na bai ɗaya, sai kuma sun bambanta daga wannan ƙasa zuwa wata ƙasar. Amma dai batun amfani da Faransanci gaskiya ne cewa ya bambanta sosai musamman idan aka yi lakari da matsayin da harshen ƙasa ya ɗauka a ƙasa, amma kuma kamar yadda aka samu a birane (Taswira " Matsayin shirin samar da hadin kai tsakanin ƙasashe masu magana da harshen Faransanci").

## HANGEN FARANSANCI TA CIBIYOYIN SARRAFAWA MASU YAWA

Bincike na kwana-kwanan nan da Cibiyar Kanta ta gudanar wanda muka iya yin amfani da sakamakon, wanda kuma ya shafi ƙasashe guda goma sha biyar[10] an gudanar da shi ne a cikin wata ukun farko na shekarar 2020 da kuma wata ukun farko na shekarar 2021. Sakamakon binciken ya nuna ilmin Faransanci mai yawa amma kuma wanda ya sha bamban a duk ƙasashen da aka yi amfani da su wajen gudanar da nazarin.Yawan jama'an da suke wa kansu laƙabi da Faransa su suke da rinjaye da kaso tsakanin 57% (a cikin garuruwan Senegal) da kuma har kashi 90 % (a biranen Congo), amma ƙwarewa a harshen ya shafi mutane ne ƙalilan. Kamar yadda wata manuniya da Kantar suka tsara na waɗanda suka ƙware a Faransanci, za a iya ganin kaso har 28% (a Burkina Faso) da kuma 68% a biranen Aljeriya).

Idan aka yi la'akari da juye-juyen zamani, mun fahinci akwai alamun daidaito a kan yawan masu magana da harshen Faransanci da ake samu a cikin al'umma. Bincike na can baya da muka yi kamar a shekarar 2008, wasu abubuwa na koma baya suka sa muka yi wannan hasashe. Idan mafi yawan ƙasashen da abin ya shafa ba su sami wani muhimmin canji ba a rahotonsu na yawan masu magana da harshen Faransanci da kuma waɗanda ake ganin suna da ƙwarewa wajen magana da harshen Faransanci, za mu iya ganin wasu abubuwa kama haka:

Mutanen Gabon da na Marocco sun nuna ƙaruwar masu ƙwarewa da magana da harshen Faransanci cewa kowa da kowa ne. Su ma waɗanda ba su ƙware sosai ba ƙaruwa suke a biranen ƙasar Côte d'Ivoire. Shi kuma adadin masu magana da Faransanci baina-baina bai canza ba. Birane ƙasashen Mali da Tunis su ma sun nuna ƙaruwa na mutanen da suke kallon kansu a matsayin masu magana da harshen Faransanci a tsakanin shekarar 2020/2021 da kuma 2021/2022 (ƙarin ɗigo 17 da ɗigo 18). A wani ɓangaren idan aka rage yawan harshen Faransanci a cikin biranen DRC, za a rage yawan masu ƙwarewa wajen magana da Faransanci da kashi 7 cikin ɗari a tsakanin shekarar 2009 da kuma shekarar 2020/2021. A biranen ƙasar Senegal kuwa abin da aka samu gaba ɗaya kishiyar bayanin baya ne, adadin da ake da shi na masu magana da Faransanci bai canza ba sai dai ma raguwa da aka da waje kashi biyar tsakanin 2009 da kuma 2020/2021.




### Matasa ne ne ke da rinjaye

Mafi yawan masu magana da Faransanci a ƙasashe Afrika Kudu da Sahara za a samu matasa ne 'yan shekaru 15 zuwa 24. Wannan ya bayyana akwai yiwuwar samun haɓakana masu magana da harshen Faransanci. A zahiri, sakamakon ya nuna cewa akwai yiwuwar waɗannan matasa su kasance masu ƙwarewa wajen magana da harshen Faransanci fiye da manyansu. Idan aka cire ƙasar Mali da Rwanda da Togo, ya ɗan shafi Congo da DRC kason matasa daga ƙauyuka da ke magana da harshen Faransanci ya fi yawa fiye da na sauran al'umma. Tazarar da ke tsakani ya kai kusan ɗigo 6 amma a ƙasashe 4 a wani lokaci kashi 10 zuwa 20. Wannan a zahiri tabbaci ne na ci gaba da rayuwar harshen Faransanci wanda muka riga muka gano a sakamakon wasu bincike da ya nuna ƙaruwa na amfani da harshen Faransanci a tsakanin matasa.

Baya ga matasa, masu magana da Faransanci a birane mafi yawa mutane ne masu matsakaicin ilmi a ƙalla matakin ilmin Firamare, sai dai wani lokaci akan sami masu ilmin Sakandare da ma na gaba da Sakandaren, ke nan yana wurin da za a ce yana cikin al'ummar da za mu iya cewa akwai kwanciyar hankali. Mun ga muhimmancin makaranta a nan, wanda shigarsa ya danganta ne da yadda ake samun kuɗin shiga, wanda shi ma yana da alaƙa da matsayin mutum a cikin al'umma, ga kuma hulɗoɗin al'umma da harkokin al'ada da kuma wararen aiwatar da sana'a. Duka waɗannan suna da alaƙa da yawan amfani da harshen Faransanci da kuma ƙwarewa

[7] PASEC2019. Qualité des systèmes éducatifs en Afrique subsaharienne francophone. Performances et environnement de l'enseignement-apprentissage au primaire. Duba qrcode.

[8] Bénin, Burkina Faso, Burundi, Kamaru, Kongo, Côte d'Ivoire, Gabon, Guinea, Madagascar, Niger, Jamhuriyar Demokradiyyar Kongo, Senegal, Chad da Togo.

[9] Kimantawa sun shafi ilimin firamare ne kawai.

[10] Moroko, Algeriya, Tunisiya, Mauritaniya, Jamhuriyar Central Africa, Togo, Rwanda, Senegal, Cote d'Ivoire, Kamaru, DRC, Gabon, Mali, Burkina Faso, Kongo

### ■ Mazaunin harshen Faransanci

Alaƙa tsakanin ƙwarewa a harshen Faransanci da kuma damar da hakan kan bayar ya bayyana ƙarara a amsoshi masu alaƙa da muhimmancin wannan harshe da alakarsa da sauran darussa. Saboda haka harshen Faransanci daidai yake ko kuma a ce ana masa kallon tubarkalla saboda yadda yake ruwa ya yi tsaki wajen yin:

- Samar da aiki (tsakani kashi 67 da kashi 97 cikin ɗari na ra'ayi).
- Nazari (tsakanin kashi 68 da kashi 98 cikin ɗari).
- Samar da bayanai (tsakanin kashi 49 da kashi 98 cikin ɗari)
- Bincike a yanar gizo (tsakanin kashi 53 da kashi 97 cikin ɗari)
- Samun bayani game da wasu al'adu (tsakanin kashi 55 da kashi 96 cikin ɗari).

### ■ Harshen Faransanci a matsayin harshe na biyu

Matakan da aka ɗauka na amfani da harshen Faransanci an ɗauke su ne ta hanyar tambayar da aka yi na sanya harsunan da ake amfani da su a gida da wajen aiki cikin rukuni da kuma rarrabewa tsakanin waɗanda ake yawan amfani da su (babban harshe) da sauran dangane da wanda ya fi muhimmanci.

**A wajen aiki**

Faransanci na nan a ko'ina. Akan ma same shi a sahun farko (harshen farko) a biranen Cote d'Ivorie da Kamaru da Congo da Gabon (wurin da da shi ne ma kawai harshen da aka ambata) da kuma DRC. A duka sauran ƙasashen idan ban da Burkina Faso (harshen Moore da Dioula suna gabanta) da Rwanda (bayan harshen Kinarwanda da Ingilishi) harshen Faransanci shi ne harshen mulki na biyu da ake amfani da shi a biranen.

**A gida**

Yin amfani da harshen Faransanci a gida a koyaushe yakan kasance bai kai yawan yadda ake amfani da shi a wajen aiki ba, Wani lokaci ma ɓacewa yake yi kamar a biranen ƙasar Senegal da Mauritania. Sai dai duk da haka matsayin darajarsa a cikin harsuna na nan ba ya girgiɗi. Ana ma iya samun Faransanci a matsayin harshen farko a ƙauyukan Cote d'Ivoire da Kamaru da Congo da Gabon. A biranen ƙasashe da yawa shi ne harshe na biyu da aka fi amfani da shi kamar a Mali da Aljeriya da Afrika ta tsakiya da DCR da kuma Togo. Daga ƙarshe, a kasar Moroko da Tunisia da kuma Rwanda matsayin harshen tsaka-tsaki ne, yana ɗaukar matsayin harshe na biyu ne ko na uku, ana amfani da shi wajen sadarwa a cikin iyali.

**A taƙaice sakamakon binciken ya bayyana waɗannan hasashe:**

→ Duka ƙasashe rainon Faransa da ke wannan shiyyar suna amfani da harsuna masu yawa, kuma babban harshensu ba dole ba ne ya zama Faransanci;

→ Iya yin harshen Faransanci na bukatar himma da ilmi, idan aka manta da batun ƙwarewa wanda yake ana samunsa ne a cikin al'umma kalilan;

→ Matsayin Faransanci na harshen mulki bai sa harshen ya kasance yana haɗuwa a ko'ina ba, ko kuma a ce an ƙware wajen amfani da shi ko kuma ma yin amfani da shi gaba ɗaya ba ;

Matsayin Faransanci na musanman (ba tare da an yi daidai tashi da wasu harsuna na kasa da kasa ko na kasa) da wannan harshe yake dashi a cikin al 'ummomi , ya bashi darajar harshe Afirka,wandan masu magana dashi suka mallaka

→ Wasu da suka sa harshen ya kafu kuma da ke sa ci gaban harshen (yadda matasa suka karɓe yadda ake amfani da shi a gidaje da harkokin kasuwanci) ya cancanci kulawa ta musamman.

### ■ Bambancin Zamantakewa na Faransanci

Wata tambaya ita ce wadda ta shafi hanyoyin iya yin Faransanci da amfani da shi da kuma ilminsa da kuma sauran harsuna da suka cancanci bayani sosai. Mai karatu zai sami karin ilmi a sakamakon kwana-kwanan nan da aka yi a ƙasashe kusan 12 a Afrika[11] da a ciki ake nuna yadda ake amfani da Faransanci. A tattaunawar da muka yi da Farfesa Bernard Cerguiglini, wanda yake masanin harsuna kuma shugaban gidauniyar ƙamus na Faransanci[12] ya nuna yadda wannan batu yake da muhimmanci.

(L'Observatoire de la langue française) Gidauniyar harshen Faransanci ita ta fara wannan bincike[13] a kan bambancin Zamantakewa na Faransawa, fahintar da masu magana da harshen da kuma yadda ake amfani da shi, musamman a fannin ilmi. An gayyaci masu bincike da su gudanar da bincike a kan yiwuwar « samun haɗin kai » na harshen Faransanci da ake masa kallon mallakar masu magana da ita koda kuwa suna zaune a Paris ne ko a Dakar ko Kinshasa. Idan aka yi la'akari da sakamakon bincike da tambayoyin bincike da tattaunawa da kuma sa ido na kai tsaye na azuzuwa, aikin waɗannan masu bincike ya ba su damar gano wasu halayya.

**Harshen Faransanci** ana masa kallon wani abu muhimmi, masu wannan kallon kuwa su ne waɗanda ba shi ne harshensu na haihuwa ba. An sami wannan ne cikin wani bincike mai cike da hangen nesa. Wannan batun ma haka yake idan aka zo magana a kan harshen kasa wanda yin amfani da shi ya nuna wani abu mai kama da na soja. Abin sha'awa ne a fahinci cewa, duk da kasancewar yana cikin zuciyar masu magana da shi, tarihin zuwan Faransanci nahiyar Afrika da tekun Indiya (mulkin mallaka) bai haifar da wata ƙyama ta a zo a gani gare shi ba. Koda kuwa ya zama wajibi ko kuma dole, za a iya ganin ra'ayin mutane na nuna ƙin jini koda bayan shekara 60 ne bayan samun 'yancin kai. Wannan ba yana nufin mutane ba su fahinci bukatar ƙasashe masu magana da harshen Faransanci na Arewa musamman wanda ya shafi Faransa ta ci gaba da nuna matsayinta da kuma ci gaba da mamayar da harshen Faransanci ke yi ba. Duk da haka sun amince da irin damar da ƙwarewa a harshen kan samar. Daga ƙarshe dai yawan komawa da ake yi ga harshen Faransanci, wanda aka tabbatar bai shafi yadda ake amfani da harsuna da yawa ba, wanda da ma al'ada ce na al'ummomi masu magana da harshen Faransanci na Kudu.

Kalubalen masu yekuwar yaɗa harshen Faransanci tare da masu magana da harshen Faransanci za su fuskanta zai kasance ne ya shafi yadda suke iya tallafawa yin amfani da harsuna da yawa kuma suna yaɗa Faransanci.

**Ire-iren Faransanci,** wanda ya isa ya ƙaryata wannan, duk da haka kuma ba a maganarsu. Masu maganar ba su da yawa saboda haka ba sa iya fahintar amfaninsu da kansu, amma kuma sun tabbatar da cewa da su da kuma yadda ake amfani da su. Baya ga wahalar da suke fuskanta wajen bayyana yanayin irin wannan harshe – har da su kansu masu bincike da suka buga tambayar, akwai turjiya wajen amincewa da shi. Sai dai bayanan da suka shafe su tare da batun a cikin harkar koyarwa, ya nuna bukatar a fahinci wannan magana, kuma a amince da cewa akwai Faransanci iri-iri. Wannan abu yana da mazauni a makarantu, ko da kuwa mafi yawan malamai na koyar da karɓaɓɓen Faransanci ne a aji, a ciki ne lokaci zuwa lokaci suke nuna ire-iren Faransanci (da ma harshen ƙasa) muddin dai ana amfani da su wajen hulɗa da neman ilmi. Duk da haka kuma suna da shakku a kan ingancin musamman ma muhimmancinsa musamman a kan abin da ya shafi sakamako, yin amfani da Faransanci iri-iri domin samun nasarar ɗalibai.

Akwai hanyar da ta kamata da malamai su bi in har ana son haka, shi ne ta hanyar gano abubuwa masu kyau, waɗanda ba za a kira shi da haramtacce ba, muddin dai za su samar da koyarwa mai inganci…

## HARSHEN FARANSANCI DA AMFANI DA HARSUNA MASU YAWA A MANYAN ƘUNGIYOYI NA DUNIYA.

### ■ Haɗarin harshe ɗaya

Rahotanni daga ƙungiyoyin duniya da kuma masu sa ido na duniya duka sun amince cewa yin amfani da harshe na ƙara ja baya daga amfani da harsuna da yawa. An gabatar da bayanai da yawa masu tagomashi ga harshen Ingilishi, amma kuma masa haka ga harshen ƙasa ko harshen aiki a duka waɗannan ƙungiyoyi, musamman wajen ɗaukar aiki da sadarwa na waje da kuma kiraye-kirayen tayin yin ƙwangila.

Rahoto na ƙarshe na babban Sakataren Majalisar Ɗinkin Duniya a kan yin amfani da harsuna da yawa ya jaddada wahalhalun da ake fuskanta wajen aiwatar da amfani da harsuna masu yawa. Harshen Ingilishi shi ne a sahun gaba a Majalisar Ɗinkin Duniya da wajen ɗaukar aiki—Kaso 98.7% na waɗanda aka ɗauka aiki an dage a kan cewa sai suna da ilmin Ingilishi. Yayin da Faransanci ya nuna na kashi1.2 tun shekarar 2017 (a kashi10.4%), A sadarwa na cikin gida kuma akwai kashi 98% na abubuwan da ƙunshe a ciki cikin headquarter yana nan cikin harshen Ingilishi (shi ne karin kashi 23 tun 2018) akasin na Faransanci da ke da kashi 16%.

Harɗaɗɗiyar cibiyar bincike (ICC) na Majalisar Ɗinkin Duniya[14] ta nuna a cikin rahotonta na baya bayan nan cewa akwai rashin ci gaba da kuma bukatar majalisun zartarwa su ɗauki matakai na tabbatar da samun daidaito tsakanin aiwatar da ingantaccen shirin amfani da harsuna masu yawa da kuma samar da kuɗaɗe kamar yadda ya dace.

A Kungiyar Tarayyar Turai ma maganar ba ta canza zani ba a kan batun yin amfani da harsuna da yawa: Tsakanin 3.7 % (A tarayyar Turai) da 12 % (a majalisar Turai) na takardun da aka samar suke rubuce da Faransanci, wanda haka na nuna ci gaba da raguwa har na tsawon shekar 20 a lokacin da yake akwai kaso 34% (a 1999).

Ya ma fi muhimmanci a dakatar da waɗannan ɓatancin, tun da idan aka yi la'akari da binciken da aka gudanar 25 % na

[11] Algeriya, Benin, Kamaru, Cote d'Ivoire, Ghana, Labanon, Moroko, Madagascar, DRC da Chad.

[12] Duba qrcode.

[13] « Pratiques et représentations sociolangagières des français en Francophonie » (PRESLAF). Le rapport complet et les résultats de l'étude peuvent être consultés à l'adresse suivante. Duba qrcode.

[14] Rahoton ya ƙunshi nazari mai zurfi da ƙididdiga na bayanai daga takardun da aka tattara, martani ga tambayoyin (fiye da hirarraki 100 da wakilan hukumomin Majalisar Dinkin Duniya da ke Geneva, New York, Paris, Rome da Vienna da kuma tashoshi biyu wadanda ba na hedikwata ba: Brussels da Nicosia).

jama'ar Turai suna ya fahintar abinda aka rubuta a shafin jarida ko wani sauti mai hoto na harshen Ingilishi[15] kuma tun daga ficewar Ingila daga Tarayyar Turai, kasa da 1% na al'ummar ƙasashen harshen Ingilishi ne harshensu na haihuwa….

Abin da Majalisar Ɗinkin Duniya da Tarayyar Turai suka gano kusan ɗaya ne da sauran yankuna da kuma ƙungiyoyin duniya kamar aka gani a takardun shirin sa ido da aka gudanar na bayan nan mai suna Vade mecum de la Francophonie na IOF wand ya shafi Tarayyar Afrika da majalisar Turai da ma majalisar gudanarwa ta Turai.

## ■ Damar samar da tsari mai hawa uku wato sa-ido, da ƙararrawa da aiki

Dagewa wajen « dakatar da koma bayan da ake samu na yaɗuwar harshen Faransanci », Babban Sakatare na Shirin Samar da Haɗin kai tsakanin ƙasashe masu magana da harshen Faransanci Mrs Loiuse Mushikwabo, ta samar da wani babban shiri da ya ƙunshi wakilai jihohi da gwamnatoci a « harshen Faransanci » domin gudanar da aiki, Ita ce ta yi wannan shiri kuma take shugabantar tarurrukansu a kai a kai.

Sa-ida da « kaɗa ƙararrawa da yin aiki da aka yi domin harshen Faransanci da kuma yin amfani da harsuna masu yawa a ƙungiyoyin duniya » da kuma ke samun tallafin ƙasashen rainon Faransa an gabatar da shi domin ya samar da sauƙi waje harkokin sadarwa da musayar ra'ayi da sauran abubuwa da suka shafi harkar yanar gizo na harshen Faransanci. Yanar gizo da ita ce mahaɗa an samar da ita ne domin sa ido da gargaɗi a kan wani abu da ya saɓa tsarin harsuna na ƙungiyoyin duniya.

**Shawarar siyasa da jawo hankulan ƙasashe da gwamnatoci**

Daga babban ofishinta na Paris tare kuma da wakilanta na waje[16] musamman waɗanda ke aiki da ƙungiyoyi, OIF tana da ƙudurin bayar da shawarwari a matakai daban-daban kuma a kan harkoki daban-daban wanda a cikinsu akwai ƙungiyar jakadan ƙasashe masu magana da harshen Faransanci (GFA) da kuma tarin ma'aikatan hukuma na duniya. Shi kuma babban Sakatare a koyaushe jawo ra'ayi yake yi a manyan wurare kamar shugabannin Gwamnati da shugabannin manyan ƙungiyoyi na duniya har zuwa ga Majalisar Ɗinkin Duniya.

Tare da godiya da irin tallafin da wakilan ƙasashen waje na OIF, tarurruka masu yawa da ƙudurori sun samar da ƙarfin guiwar a kan rawar da GFA ke takawa dangane da batun amfani da harsuna masu yawa. OIF ta samar da wata manhaja da za ta shigar da wannan shiri ga kafofin duniya tun farkon 2022.

## ■ Haɗa gwiwa da OIF

**Haɗa guiwa da ƙungiyoyin cikin gida da na waje (RIO)**

Haɗin kai tsakanin OIF da RIO domin tallafawa amfani da harsuna masu yawa ya haifar da wani ƙuduri kamar ƙaddamar da rubuce-rubucen kimiyya da harshen Faransanci domin shugabannin Tarayyar ƙasashen Afrika a watan Mayu 2021, da samar da wani tsari na sadarwa da harkar shari'a na Faransa domin domin kotun manyan laifuka a 2021 da buga bayanai biyu na kiraye-kiraye na nuna ra'ayi domin inganta aikin ma'aikatan Gwamnati a Faransa da samun ƙwarewa wajen amfani da harshe (an zaɓi shirye-shirye guda 9 da waɗanda za su amfana da su guda 8 daga RIO).

**Horarwa da inganta aiki**

Domin gina ingantattun tsare-tsare na horar shugabanni da jakadu, OIF ta ƙirƙiri wasu shirye-shirye domin haɓaka yawan shugabanni da ƙwararru a wasu ma'aikatu da aka zaɓa da suka nuna iya harshe Faransanci isasshe, su iya bayyana kansu a matsayinsu na ƙwararru. A wannan fannin ƙasashe 19 sun ƙulla yarjejeniya (shirin ƙasashe rainon ƙasar Faransa da kuma shirin Samar da muhalli na ƙasashe rainon Faransa. IFN da IFE tare da OIF domin 2019-2022. Fiye da wakilai 1200 ake horarwa a kowace shekara, kashi 70 cikin ɗari daga cikinsu mata ne.

**Shawara a kan kayan aiki da kuɗaɗe**

A shekarar 2020 OIF ta ci gaba da bayar da tallafinta ga TV5MONDE domin gabatar da shiryen labaru 42 (kwana 7 a la Planete) 1080 na horar da kai, 262 na abubuwan da suka shafi ilmi. Domin koyar da kai an yi nasarar samar da Faransanci da hulɗa da ƙasashen duniya domin ɗalibai masu ƙudurin karatun samun takardar shaidar digiri a fannin dangantakar duniya (DFP-RI) a cibiyar Kasuwanci da masana'antu. Paris Ile-de-France ko kuma Huldar jakadanci mai manufa ta gari domin gabatar da Faransanci domin hulɗa da ƙasashen duniya na yau da kullum ko kuma na akasin haka. A watan Maris 2020 TV5MONDE ta ƙaddamar da wata manhaja mai suna Koyi Faransanci a TV5MONDE wanda a ciki akwai aiki har guda 3000 a shafinsu na yanar gizo wato apprendre.tv5monde.com.

Haka kuma OIF na da alaka da Hachette FLE tun shekarar 2017 domin wallafa wani littafi mai suna Objectif diplomaie level 1 New Edition, littafi da aka tandar domin koyar da Faransanci ga jakadu. A wata Disamba 2019, an inganta littafin da wasu manhajoji na gyaran kuskure har guda 150, kana kuma a ƙarshen shekarar 2021 an saka wannan littafi na Objectif diplomatie.lab level a yanar gizo domin malamai.

[15] Eurobaromètre Spécial 386, 2012

[16] Addis-Ababa, Bruxelles, Geneva da New York, har da Antananarivo, Bucarest, Dakar, Hanoï, Libreville, Lomé, Port-au-Prince, Québec, Tunis da kuma na ba da jimawa ba, Beyrouth.



**Mayan mahaɗai « Zaman lafiya da tsaro »**

Domin ƙarfafa kasancewar masu magana da harshen Faransanci a PKO da Majalisar Ɗinkin Duniya (An ƙiyasta 27% a watan Janairu2021, yayin da mafi rinjaye na ayyuka ana kai su zuwa wuraren da suke matsayin rainon Faransa) OIF ta gudanar da ayyuka da yawa waɗanda suka haifar da kyawawan sakamako. ɗaya daga cikin irin waɗannan ayyuka shi ne na haɗin guiwar OIF da UN domin ƙara ƙarfafa harkar koyar da Faransanci ga sojojin MINUSMA[17] (Mayu, 2021).

A matsayin ayyukan haɗin guiwa da OIF ton yi da wani sashe na 'yan sandan Majalisar Ɗinkin Duniya, an yi taron ƙara wa juna sani guda biyu a ƙasar Paris da Bamako a 2021 tare da tallafin cibiyar horar da 'yan sanda na Faransa domin ƙara inganta waɗanda ake gabatarwa domin aikin 'yan sanda. An lura da ƙaruwar yawan 'yan sanda daga yankunan da za a kira rainon Faransa daga kashi 28% a 2012 zuwa kashi 80% a 2021.

Idan kuwa a kan batun kwasa-kwasan horar da masu magana da harshen Faransanci ne, za mu iya kawo batun shirin horar da masu magana da harshen Faransanci na farko da aka shirya domin ofishin Jakadanci na farko wanda har yanzu ana yi da harshen Ingilishi. Ga kuma ajin koyar da jami'an soja mata Faransanci, da kuma shirya kwas da harshen Faransanci domin masharwan soja na PKO na daidaiton jinsi (EFH)

Wani abu da aka yi nasara kuma shi ne wanda aka ƙaddamar a 2021 a dandalin REFOP, wanda yanzu an saka shi a yanar gizo Boutros –Ghali na tabbatar da ci gaban zaman lafiya. Wannan hanyar sadarwa[18] na amfani da ƙwarewar harshen Faransanci da makarantu da cibiyoyin horarwa domin tabbatar da ɗorewar zaman lafiya kuma suna nan an ɗora su a yanar gizo.

**Faransanci a matsayin harshen Wasanin Olympic da Wasannin Masu Nakasa (OPG)**

A kowane wasa za a gudanar, OIF takan samar wa Kwamitin shirya gasar Olympic wani jami'i ƙwararre a Fassara a tura shi sashen ilmin harsuna da sahen yaɗa labarai wanda zai taimaka wajen fassarawa da rubuta bayanai cikin harshen Faransanci. Tun a shekarar 2004, Babban Sakataren shirin haɗa kan ƙasashe rainon Faransa ya ɗora wa wani alhakin yin haka. Yin hakan kuma yin biyayya ne sashe na 23 na yarjejeniyar Wasannin Olympic[19]. Aikin gudanar da babban gasa mai lakabin Temoin de la Francophonie na 2020 a ɗanka shi hannun Thierry Marx, wani sanannen masanin girke-girke.

## ■ Zuwa ga ƙarin yin amfani da harsuna masu yawa?

**Ci gaban Majalisar Ɗinkin Duniya**

Sashen kula da al'umma na majalisar Ɗinkin Duniya ya kammala rubuta kundin da ke ɗauke da tsarin ma'aikatan majalisar a 2020 domin ƙarfafa shirin tabbatar koyon harsuna guda shida[20] domin tabbatar da ƙwarewa cikinsu. Aiwatar da wannan shirin ya samar da wani sabon launi ga tsarin kwasa-kwasan harsuna na matakai daba-daban da kuma yadda ake amfani da su. A hankali wannan tsari zai ingantu wajen ƙafa irin harsuna ko harshen da ake so mutum ya iya kafin a ɗauke shi aiki.

Babban ofishin Majalisar Ɗinkin Duniya ya sanar da sabbin wasu shirye-shirye masu sauƙi a kan yin amfani da harsuna masu yawa a 2022, kamar **shirya tsare-tsare na samar da siyasa mai inganci** da zai ba da damar shigar da harsuna masu yawa cikin ayyukan Majalisar Ɗinkin Duniya. OIF tana tallafawa ayyukan ci gaba ta hanyar gudummuwar da take samu da samar da ƙwararru a matakin shugabanci.

**Muhawara na kwana kwanan nan na Tarayyar Turai**

Tun fitar Burtaniya daga tarayyar Turai, mamayar harshen Ingilishi na ƙara samun tagomashi. An ɗaga muryoyi da dama[21] a nuna rashin amincewa da amfani da harshen da ba harshen ƙasa ba ne. A ƙasashe biyu ne kawai Ireland da Malta kawai ake amfani da shi. Tattaunawa a kan yin amfani da harsuna da yawa a Tarayyar Turai ya ƙara tasowa tare da matsalar cuta da ta taso ta saka gaba ɗayan ƙasar Turai cikin ruɗani wanda ya sa su yin amfani da da taron ta hanyar yin amfani da bidiyo da harshen Ingilishi a mako na farko, a kowane mataki a cikin har da babban taro. Daga Mayu 2020. Tarayyar Turai sun kafa wata kafa ta yin hulɗa ta hanyar yin amfani da harsuna 32. Daga ƙarshe wakilin Faransa na Tarayyar Turai a mataki da ya zama shi ne hanyar da za kawo sabbin tsare-tsare cikin tattaunawa da ke nuna goyon bayan sake duba matsayin harshen kasa.

[17] Mission multidimensionnelle intégrée des Nations Unies pour la stabilisation au Mali

[18] Duba qrcode.

[19] Sashe na 23 na yarjejeniyar Wasannin Olympic : Harsunan hukuma na IOC sune Faransanci da Ingilishi. A duk zaman, dole ne a yi fassara cikin Faransanci, Ingilishi, Jamusanci, Ispaniyanci, Rashanci da Larabci.
Idan aka sami sabani tsakanin rubutun Faransanci da na Ingilishi cikin yarjejeniyar Wasannin Olympic da na kowace daftarin aiki na IOC, rubutun Faransanci zai yi nasara sai dai idan an ba da sanarwar in ba haka ba a rubuce.


[20] Duba qrcode.

[21] Za mu iya buga yunƙurin ƙungiyar ma'aikatan faransanci na Turai, mai suna «Carré bleu», wanda ya aika budaddiyar wasika zuwa ga Shugaban Hukumar a watan Satumba na 2019 yana neman hakkin yin aiki da Faransanci.

SASHE NA 2

# MANUFOFIN HARSHE DA KOYARWA DA HARSHEN FARANSANCI DA KUMA KOYAR DA FARANSANCI A DUNIYA

# FARANSANCI A MATSAYIN HARSHEN KOYARWA



## FARANSANCI A MATSAYIN
## HARSHEN KOYARWA

Faransanci shi ne harshen da ake aiki da shi a fannonin ilimi a ƙasashe da gwamnatocin ƙasashe talatin da shida a duniya (ƙasashe ashirin da huɗu suna Afirka da Tekun Indiya da kuma Gabas ta Tsakiya). Ana aiki da Faransanci shi kaɗai ko tare da waɗansu harsuna; kashi tamanin cikin ɗari na ɗalibai da suke shiga makarantun harshen Faransanci suna Afirka ne inda Faransanci ne kawai ake aiki da shi; Duk da cewa Faransanci da shi ake aiki akwai sadarwa a tsakanin jama'a masu jin wani harshe ko harsuna saboda bambancin al'adu da harsuna).

### ■ Zaɓen Tsarin Harshe da Matakan da ƙasashe ke ɗauka

Kasashe da gwamnatocin ƙasashe renon-Faransa musamman ƙasashen Kudu da Sahara da na Tekun Indiya, suna buƙatar tsare-tsare da zai yi la'akari da walwalar da suke yi ta zahiri da harsuna ta yada za a yi tsarin harshe da zai mutunta bambancin: harshe da damakaraɗiyya da kananan harsuna da kuma koyar da ilimi ta amfani da harsuna biyu , da samun aikin yi da raya ƙasa da hulɗa tsakanin jama'a da kuma al'umma da faɗakar da kowa da kowa da kuma 'yancin yin amfani da harshen dangin uwa, da sauran su.

Shaihun Malami Jean Marie Klintenberg na jami'ar Liege dake ƙasar Belgium, ya bayyana cewa; "Tsare-tsaren harsuna wani ginshiƙin abu ne a ci gaban mutun shi kaɗai ko ci gaban al'umma idan ta samar da harshe ɗaya ne da za a yi aiki da shi domin samun ƙwarewa wajen bayyanawa (. . .) a haɗa shi da tsarin ba da horo da tsarin kiyayewa da ci gaban ma'aikaci (ta nuni da harshen da tsaro) da tsarin kwantaragi tsakanin 'yan ƙasa da hukumomi (ta fuskar saukaka aikin hukuma da harshen shari'a da sauransu). Zuwa tsarin bincike da raya ƙasa musamman a hanyoyin sadarwa na zamani da tsarin ba'yan ƙasa damar samun dabarun bayani da sadarwa".

Akwai ƙudurori da rubuce-rubuce masu yawa don kare bambancin harshe da suka haɗa da tsarin harshe na ƙasa a ƙasashen Afirka masu yawa (Misali a Afirka ta kudu) ko a tuna da tsarin amfani da harsuna biyu ko fiye da haka na koyar da ilimi don bunkasa koyo a matakin farko (Misali, Mali, Burundi) Sannan akwai mataki na ƙasa da ƙasa da aka cin ma don a kare dukkan harsuna da matakan da ake ɗauka saboda a kare harshe daga "wasu ƙalubale a muhalli da yake wanzuwa". Sai dai a zahiri abu kaɗan ake yi game da tsare-tsaren kuma sun shafi matsayin harsuna ne, (matsalolin wannan hali a bayyane suke kuma abin da suke haifarwa kaɗan ne kuma ba bu kyakkyawan dubawa).

Ta wani ɓangare, idan aka samar da abubuwan da aka rubuta kuma ƙasashe da masu ruwa da tsaki suka biya kuɗin shirye-shirye, yakan shafi gabatarwa ne kawai game da wasu harsuna ne a fagen ilimi da ilimantarwa musamman a matakin farko. Duk da haka, tsarin harshe abubuwa ne da jihohi ke aiwatarwa ta la'akari da iyakokinsu sannan a raba su a ƙarkashin kulawar hukumomi daban daban a ƙasashe daban dabam.

A irin wannan hali ne ƙasashe renon Faransa sukan taimakawa junansu da gwamnatoci ta gudanar da shirye-shirye a kan tsare-tsaren harsuna da ilimi, da sanin makamar aiki ga malamai, tantancewa game da koyo da zai amfani koyar da ilimi ta harsuna biyu (musamman ta tsarin makaranta da hukumar harsuna a Afirka wato ELAN).

### ■ Halin da ake ciki a yanki da ƙasa


An yi ƙiyasin akwai ɗaliban firamari da na sakandare guda **miliyan casa'in da uku (93)** da ake koyar da su da harshen Farasanci a duniya; kuma wannan adadi ƙaruwa yake kaɗan-kaɗan, sannan an nuna cewa Faransanci bai rasa matsayinsa ba na harshen da ake amfani da shi a ko ina, kuma game da harkokin ilimi a ƙasashen da yara ke zuwa makaranta ke ƙaruwa (misali a Kudu) yawansu ƙaruwa yake (ko da ba dukansu suke zuwa makaranta ba).

A ƙasashen da Faransanci shi ne kaɗai harshen hukuma a duniya, mafi yawan masu koyon harshen Faransanci suna ƙasar Afrika ne har da ƙasashen da Faransanci ba shi ba ne harshen hukuma ba (misali a Arewacin Afirka).

Kasashen Turai ne na biyu, a godewa ƙasar Faransa, yara (9,120) masu zuwa makarantar Faransanci ne, ga Wallonia –wato tarayyar Brussels, ga masu magana da Faransanci a Switzerland ; da Luxemburg da Monaco.

Idan Arewacin Amurka ya zama na uku zuwa Quebee da Canada gaba ɗaya, ba za a manta da matsayin Haiti ba, ko da kuwa ƙididdigar a wannan ƙasa sun tsufa wato na shekarun (2015-2016) ne. A ƙarshe, ƙasar Labanon ita ta mamaye a yawan makarantun Faransanci a Arewacin Afirka zuwa Gabas ta Tsakiya. Inda matsyin harshen na wanda ake aiki da shi ba abin yarwa ba ne duk da cewa babu takamaiman ƙididdiga a ƙasashen Arewacin Afirka.

A yankin Asiya, rashin yawan masu koyon Faransanci a ƙasar New-Calendonia da Vanuata ya sa da wuya a san yawan adadin masu koyo.




## FARANSANCI A MATSAYIN
## HARSHEN ƘASAR WAJE

Yawan ɗalibai masu koyon Faransanci a matsayin harshen ƙasar waje ya bambanta a yankuna ko ƙasashe, kuma wannan ya danganta ne da abin da hukumomi suka tilasta wajen koyar da harshen ƙasar waje na biyu (ko fiye) a cikin harkokin ilimi. A wajen ƙasashe masu magana da harshen Ingilishi an lura tsare-tsare na jama'a yakan bar Ingilishi ne a matsayin al'adar harshe ta yi zaman kanta a wajen horar da matasa 'yan ƙasa.

Abin sha'awa game da harshen Faransanci ga matasa da iyayensu da makarantu shi ne saboda damar da ake samu ta samun aiki, damar yin karatu a ƙasashen waje, samun damar ayyukan da suka shafi yawon shakatawa, ƙungiyoyin duniya ko haɓakawa a cikin ƙamfani ko gudanarwa.

Mataki na siyasa yana da matsayi sosai wajen gina tsare-tsaren ilimi da al'ummomi masu yawan harsuna da zai kawo ci gaban ɗaukan matasa aiki da koyarwa tare da bunkasa rayuwa. Kuma a yi la'akari da matsalolin da tsarin ilimi yake fuskanta, waɗanda wani lokaci na yawan masu koyon Faransanci da kuma ƙarancin malamai, da kuma yadda malamai ke ajiye aiki ko yin ritaya (ko shi ya isa ya hana koyar fa Faransanci a makaranta); matsala ce ta koyar da harsuna (har da Faransanci) wanda dama ta ganin da mace da ta shafi harshen ƙasashen waje na biyu.

### ■ Koyon faransanci a tsare-tsare ilimi mai harsuna da yawa

Ilimi da tsare-tsaren harshen na taka muhimmiyar rawa a koyon harsunan ƙasar waje, ba don tilastawa da manhaja ta yi ba har da irin nauyin da aka ɗora a kansu. Sake duba aiki koyarwa da sake ba da damar samun horo a wasu manyan birane da sa harkar dumokaraɗiyya a ba da damar samun horon harsuna da yawa suna daga cikin ƙalubalen dake sa tsare-tsaren ilimi su kula da buƙatun jama'a na mu'amala.

Haka kuma tsare-tsare na ƙasa da ake zaɓe maimakon tsarin harsuna a cikin ƙasa, yana da babban tasiri a fagen tsarin ilimi, misali game da amfani da shi a ƙasa da ƙasa.

Ta haka ne ma wasu jihohi suke buƙatar sauye-sauye da yawan yarjejeniyar taimakon juna a madadin sabunta zirga-zirgar malamai, da ƙarfafa dabarunsu na sanin harsuna, da gudanar taimakon tsare-tsaren harshe da zirga-zirgar ɗalibai da sauransu.

### ■ Yarjejeniyoyin taimakon juna game da koyon faransanci

Yarjejeniyoyin da ake sa wa hannu tare da ƙasar Faransa galibi su ke zubar da koyar da Faransanci. A tsarin yarjejeniyar ƙasar Faransa ke ba da gudumawar kuɗi makatan da ake ɗauka daga ƙananan hukumomi zuwa ƙasa da yanki FSPI (Asusun Haɗin kai don Kirkirar Ayyuka, Kungiyoyin Jama'a, Francophonie da Ci gaban Dan Adam) don gudanar da aikace-aikace na raya cigaban al'ummomi; ta makarantu da gudanar da bincike.

A ɓangaren taikamon juna na Faransa, (a faɗan **le Label FrancÉducation**) za a iya ba da misali da hukumar ilimi da masu taimakon harshe dake Faransa da ƙasashen waje. Har wayau Faransa tana zaburar da ƙungiyoyin dake taimakon ilimi kamar France Éducation International (FEI) a madadin ƙarfafa Faransanci a ma'aikatun gwamnati da masu zaman kansu na tsare-tsaren ilimi na ƙasa a makarantun Fansanci da aka yarda da su a ƙasashe.

A shekara ta 2020, **le Fonds Langue française** (Asusun tallafawa Faransanci) ya tallafawa ayyuka guda 29 da cibiyar koyar da Faransanci ta gudanar da Alliance Française da kuma Instituts français, waɗanda suka haɗa da haɗin guiwar Faransa da Brazil don yawon buɗe ido na Faransanci; da taron masu ba ilimin Faransanci na Bulgaria, da masu aikin taimakawa makarantu a Amurka« Les petits penseurs » (Kananan masu tunani) a cikin Amurka, an yi nufin masu sauraron makaranta.

Duk da ofisoshinta guda 98 da ƙasashe 95 l'Institut français ita ke jagorancin IFprof wadda ta tattaro ƙwararru guda 42,000 daga ƙasashe 100 wanda aka ba kayan aiki (20,000) na ɗakin karatu na zamani da ya amfani fiye da mutane 500,000 a shekara ta 2021 (wanda ya mika yawansu 2019).

A lura da cewa halattar darasin ilimin Faransanci na (FLE) a kashi na 832 na Alliances françaises a ƙasashe 131 da masu koyon FLE guda 490, 000 a duniya a shekara ta 2019 (tare da masu koyo guda 111,000 a kanfanoni ko cibiyoyi) ya ƙaru da giye da (+3.4%) tun a shekara ta 2018; ƙasashen: Madagascar da Indiya da Amurka, da Mexico da Faransa suna ƙasashe biyar na farko inda ake koyon Faransanci a cibiyoyi, sannan sai ƙasar China da Brazil da Colombia da Peru da Zimbabwe ga kuma masu ɗaukar darasin Faransanci masu yawa koyaushe a 2019, ga kwasakwasai na ma'aikatu da masana'antu nan ana ta yi a duk shekara da suka ƙaru da fiye da (+16%).
Yankin Latino Amurka shi ne a sahun farko da yawan masu koyo 130,000 da aka yi wa rijista a kashi 172 na ofisoshin Alliances Francaises a duniya mai ofishi 236.

A nata ɓangaren, cibiyar OIF tana da cibiyoyi ne masu ba da babban horon sanin makamar ba da horo da yadda ake gabatar da muƙalolin ilimi na fannoni daban-daban na koyar da Faransanci a tsarin ilimi. Wannan tsarin da aka fara gwada shi a 1993 a Asia-Pacific (CREFAP). A shekara ta 2005 an kai shi Tsakiya da Gabashin Turai (CREFECO) daga shekara ta 2021 aka kai shi Afirka da Gabas ta Tsakiya (CREFA).
Manufar shirin shi ne ya kai ga fiye da malamai 50,000 da kuma masu koyon Faransanci fiye da 4,000,000.

## Shedar sanin makama a harshen faransanci

A cikin tsare-tsaren da aka samar na tantance malamai, na APPRENDRE EV@lang- wanda FEL ke tallafawa da AVE an ƙaddamar da shi a 2021 a tsarinsa na ba da horo da zai tantance ƙwarewar malamai a tsare-tsaren ilimi na ƙasashe 26 masu magana da harshen Faransanci.

Ko a halin korona da aka shiga, shedar sanin Faransanci ta tattaro nambobi musamman matassa da yawansu ya kai 214,221 (sun haɗa da 108,376 na 'yan makaranta fannin DELF na harshen hukuma da aka tace a tsarin ilimi na ƙasa) a shekara ta 2021, a cikin jimlar 381,597 na ɗaliban DELF-DALF. Yawan ɗalibai da suka rubuta jarrabawar DELF har yanzu ƙaruwa yake har ya yi yawa sosai a shekarar 2019, da matasa 318,474 masu rubuta jarrabawa (waɗanda a ciki 163,121 sun yi rijistar jarrabawar DELF) a cikin jimlar 519,611 na ɗalibai masu jarrabawar DELF-DALF, wannan ya tabbatar da sha'awar ɗalibai ta neman shedar satifiket na matsayin sakandare.

Makarantar DELF ta sami karɓuwa a ƙasar Italiya (ɗalibai 22% suka yi rijista a shekarar 2019) a ƙasar Jamus kuma (ɗalibai 28% ne suka yi rijista).

## Bunkasa da raba kayan koyon dabarun harshen faransanci

Ta fuskar hulɗa da ƙasashen waje game da koyar da Faransanci, kwasa-kwasan da ake ba da horo a kansu domin samun shedar difloma suna buƙatar jarrabawa ta musamman. Mai koyon irin wannan Faransanci na musamman (FOS) lalle yana bayyana wani irin sauyi ne dake nuna amfanin ilimin sanin Faransanci. Akwai irin waɗanan horo da ake bayarwa a fagen ilimi mai zurfi ta wajen ba da digiri na biyu da ake kira "na ƙwarewa".

A duk ƙasashen duniya, ga fannonin da suke maida hankali a kai: harsunan ƙasashen waje a aikace, da ƙungiyoyin al'adun Turawa da harshe da yin tafintan turon karawa juna sani, da Fassara da kuma keɓaɓɓun kalmamo da dabarun sadarwa a tsakanin al'adu (na adabi da harsuna) da harsunan zamani da sadarwa ƙasa da ƙasa da malamin harshen Faransanci da harshe da fa naurar fassara mai sarrafa kanta da sauransu.

Sannan sau tari ana, samun harshen. Faransanci a matsayin wani ginshiƙin abubuwan da ake ba da horan koyon aiki mulki, da ilimin hulɗa da ƙasashen waje da harkar jakadanci ko abinda ya shafi tsoron ƙasa (musamman a Afirka).

A ƙasashen Turai, da Arewacin Afirka har zuwa Asiya, an ba da horo ba kawai a fannonin da suke da nasaba da harsuna ba; sun haɗa da: zanen gina gidaje da aikin noma, da kayan abinci da aikin Jarida da Likitanci da Kiwon lafiya da aikin gudanarwa, da aikin injiniyan masana'antu da yawonbuɗe-ido da kasuwanci da ciniki da harkokin kuɗi da tsarin shari'ar ƙasa da ƙasa (na hukuma da mai zaman kansu); da tattalin arziki da gudanarwa da lissafi har da ilimin kumfuta da ilimin kimiyyar sinadarai da tsirrai da harkar tsare-tsare da sufuri da kimiyyar siyasa da sauransu.

Sauran kayan aiki kamar satifiket na ƙwarewa a Faransanci (DFP) wanda cibiyar kasuwanci da masana'antu ta birnin Paris, wadda ake kira "FDA-CCIP" ƙwararriya a fagen horar da masu ba da horo, da kuma bunƙasa ba da horo da ba da satifiket na ƙwarewa a Faransanci (FOS). Sukan ba da dama a ƙware sosai a iya Faransanci, musamman a sashen kasuwanci da harkokin ƙasashen waje, da yawon-buɗe-ido da karamci da sana'ar sayar da abinci ta hanyar koyar da kwasakwasai na ƙasa da ƙasa.

Cibiyar kasuwanci da masana'antu wato FDA-CCIP ta ce, yadda ake neman horon ƙwarewa a harshen Faransanci bai gushe ba duk da matsalar rashin lafiya da shafi cibiyoyin koyar da harshen. Kirkiro da yin karatu daga gida na zamani ta taimaka wajen ba da horo a zamanance.

A irin yadda ake nuna sha'awar samun satifiket na ƙwarewa a Faransanci (DEP) za a ga irin cigaban da aka samu na amincewa da cibiyoyin koyar da harshen bias tsarinta na ba da satifiket na ƙwarewa a harshen (daga 30 a shekarar 1978 zuwa 70 a shekara ta 2020). Haka kuma za a ga yadda ake sha'awar tsarin koyar da masu ba da horo domin tace shirin ba da shedar ƙwarewa a harshen Faransanci.
A cikin fiye da ɗalibai 23,000 da suka nemi gurbin karatun samun shedar (PFE) a tsakanin shekara ta 2016 da farkon rabin shekara ta 2021, kashi 72% an ba su shedar (PFE) ta kasuwanci, kashi 13% shedar (PFE) na aikin sakatare; shai 6% na yawon-buɗe-ido da karamci, kashi 5.5% shedar harkokin ƙasashen waje. Kashi 80% na ɗalibai daga ƙasar Switzerland da Faransa da Italiya da Amurka, da Egypt da Algeriya da Ispaniya da Labanon da Austriya da Rasha da Belgium suke.

Abin da aka gani ya nuna ƙasashen Turai su ne kan gaba wajen neman horan samun shedar ƙwarewa a harshen Faransanci. Kasar Kenya da Indiya da Mexico nan ma ana nuna sha'awa. Har yanzu ana buƙata a Arewacin Amurka, sai kuma 'yan buƙatar da ake da ita a yankin Asiya inda buƙatar koyon dabarun sanin Faransanci da ƙwarewa ke samun ci gaba.

A cikin dabarun koyarwa na (FOS) da aka bunkasa akwai ƙaddamar da **Cles du Francais Pro** a watan Maris 2021 na FDA- CCIP da kuma institute Francais da zai tallafawa tsarin koyar da harshen Faransanci tare da bunkasa ba da shedar ƙwarewa a Faransanci.

Samar da tashar talabijin ta **TV5MONDE** ya ba damar ƙara samun kayan koyarwa a fannoni daban-daban na ƙwarewa (kasunawanci da yowon-buɗe-ido da gidan abinci da harkar salo da zane, dangantakar kasa da kasa da diflomasiyya) da ake gabatarwa a TV5 Quebec da Canada da taimakon kuɗi daga – "office Quebecois de langue Francais". Akwai aiki da ake yi domin bunkasa kayan koyarwa da dawo da tattalin ƙwarewa ta haɗin guiwa da sashen "cite internationale de langue Franciase a Villers- Cotterests" (Faransa).

Ba a kokonton samun damar da ake ganin shedar ƙwarewa ta FOS na da ita a ƙasashen waje ganin irin canjin tsarin ba da horon samu sheda na FDA-CCIP, wannan y aba cibiyoyin koyar da harshe da ba da horo su karkasa masu koyo da kuma samar da masu koyo na ƙasa da ƙasa da ake bukata su yi aiki da Faransanci. Kamar yadda Mrs. Florence Mourthon ta ce, "Muna da manyan masu koyo kaɗan, amma matsaikata masu yawan gaske domin neman ilimi da sanin kasuwanci".

## Yawan masu koyon faransanci a yanki da kasa

A shekara ta 2018, yawan masu koyon Faransanci ya haura miliyan 5.1 na ɗalibai a makaranta da manyan koleji da manyan makarantun ilimi masu zaman kamsu da kuma yawan cibiyoyin koyar da harshen a ƙasashen waje waɗanda ba tsarin makarantaba. A yankin Arewacin Afirka zuwa Gabas ta Tsakiya akwai ɗalibai na (FLE) guda 4420, sai yankin Afirka kuda da Sahara zuwa yankin Tekun India akwai kasha (25%) sai ƙasar Turai (19%) sai yankuna Amurka zuwa Karibiyen (9%) da kuma Asiya da Oshaniya (3%).

A ko ina a duniya da ake koyar da Faransanci a duniya yawan masu koyo ya da kashi 0.1% tun a shekara ta 2018, wanda ya nuna rayuwar masu koyon Faransanci a ƙasar da kashi (-10%). A daya yankin da ba ƙasar turai ba kuwa ansami ƙaruwan masu koyon Faransancin ne.

Yawan masu koyo ya ƙaru ne sosai a ƙasashen Arewacin Afirka, saboda idan aka haɗa da na Algeriya da Moroko da Tunisiya suna da masu koyon Faransan a matsayin harshen ƙasar waje fiye da miliyan (17million). Yawan ɗaliban ya rabu ne daban – daban a matakan karatun da suke a fannoni da tsarin masu amfani da "harsuna biyu" wato "da Faransanci" don wasu batutuwa da kuma a wasu matakan karatu, amma ana mutunta cancantar "harshen waje" da ake amfani da su zuwa Faransanci a waɗannan ƙasashe.

**A ƙasashen "da ba renon ƙasar Faransa ba ne" a Afirka** akwai kashi 25% sauran ƙasashe kuwa waɗanda (ke cikin OIF ko ba sa ciki), kamar yankin ƙasar Kamaru masu magana da Ingishi da ƙasar Mozambique, ko Ghana yawan na su masu koyon suna tafiya daidai da na Uganda da Angola da South Africa ko Kenya. A Afrika kusa da hama da yawan ya ƙaru ne kamar a Angola da Ethiopiya (kafin rigimar da aka yi) har a Sao Tome da Principe da Seychelles.

**Kasar Turai** nan ne aka fi koyon Faransanci inda Italiya da Romaniya suke kan gaba (wajen yawan masu koyo) tare da Jamus da Ispaniya sai ɓangaren da ba renon Faransa ba na Belgium da Switzerland da Netherland da Greece da Portugal. Kasashen renon Ingilishi (Ingila da Irland) suna koyon Faransanci a matsayin harshen farko na ƙasar waje wanda ya ba adadin masu koyo na (FLE) fiye da miliyan 0.5.


A ƙasashe da ba renon Faransa ba ne, idan koyarwa ta ba da dama a koyar da harshe ɗaya na waje ala tilas, to shi ne Ingilishi (wanda hukumomin ilimi sukan ce ba dole ba ne amma galibi haka yake. Damar da mutum yake da ita ta barin harshensa na waje a tsarin makaranta a ƙasar Ingila galibi yana rage yawan masu koyon Faransanci na (FLE).

In ana gasar nuna fifikon harsuna a ƙasashen Turai dangane da al'ada ko kusancin muhalli da kuma matsalolin da ke shafar ko wane harshen da ake "tallatawa a kasuwa", da kuma irin ribar da harsunan za su samu ya danganta ne da tsarin da hukumomi suka yi da zai ba ɗalibai da iyaye damar zaɓar (harshe). Idan harshe na biyu ko (na uku) na ƙasar waje ba na dole ba ne gasar ta fi zafi a tsakamin harshen Ispaniyanci da Rasha da Jamus da Italiya (----) a nan Faransancin bai samun nasara koyaushe.

**Yankunan Amurka da Karibeyan** su ne na uku a fagen koyon Faransanci na FLE, Sai Kanada (ban da Quebec) da Amurka da Costa Rica da Brazil da Mexico da Argentina da sauransu. Yawan masu koyo ya ƙaru da kashi +31. 17% a wannan yanki, wanda ƙari ne mai muhimmanci na koyon Faransanci a ƙasar Costa Rica da Chile.

**A Asiya – yankin Oshaniya** yana da ƙarancin masu koyon FLE, sai dai waɗansu ƙasashen na yankin sun yi fice da yawan masu koyon (kusan 50,000) amma matsakaici ne yawan idan aka dubi yawan makaranta kamar a ƙasar Australiya da india da China da Laos da Cambodiya da Azerbaijain ko Vietnam Cambodiya da Malaysiya da Thailand da Vanuatu an samu ci gaba said an akwai rashin nasara, misali, a ƙasar Japan da Kazakhastan.

Canjin masu koyon Faransanci a matsayin harshen ƙasar waje (FLE) tsakanin 2018 da 2022 (Awon wurare) ba chanji)




# SASHE NA 3

# HARSHEN FARANSANCI DA AL'ADA A YANAR GIZO

## MATSAYIN FARANSANCI
## A YANAR GIZO

### Ci gaba a taƙaice

An inganta samfurin da aka yi amfani da shi a wancan bugun littafin ta wasu fannoni misali kyakkyawar hanyar samun data game da harshe, sharewa ko shiga wurare iri – iri na nazari ga kuma data ta masu magana da harshen na biyu a kasa da kuma kula da masu magana da harsuna masu yawa[22] tare da ci gaba da warwarar bayani. Akwai rashin tsarin da ba makawa a irin wannan aiki da neman hanyoyin da za a magance) an kuma samar da data duka a watan Mayu, 2021.

Koda yake harshen Faransanci shi ne na huɗu[23] a sadarwar Internet:

- Harshen **Hindi** shi ne biye da shi ko wataƙila ma ya wuce shi, wannan wani babban ci gaba ne.
- Tazarar da yaba waɗannan harsuna yanzu: (Portugal da Rashea da Larabci da Jamus da Japan da Malay) ta **ragu sosai**, soboda haɗuwar waɗannan dalilai:
- Yadda ake shige internet a karshe renon Faransa masu ci gaban masana'antu ya cika sosai kashi (85%) a misalce, abin da za a iya ƙarawa bai da yawa;
- Kuɗin da ake biya a digital a ƙasashe masu magana da harshen Faransanci yana da sauki a dawo da shi fiye da yadda ake shiga digital a duniya.

Wanna raguwa da ta shafi Faransanci an riga an lura da ita a wasu gwaje-gwaje da aka yi a shekara ta 2019 da 2020, ya auku ne saboda bambanci mai girma da aka samu a duniya na yadda kasa ko kasashen dake magana da Faransanci suke shiga digital. Wannan bambanci yana da girma kuma a kasashen Asiya da kuma kasashen Arab wanda yawan masu shiga ya kusa kai yawan na kasashen yamma. A hangen nesa, ana sa ran karuwar yawan jama'a a Afirka zai taimakawa amfani da harshen Faransanci a internet. Sai dai kuma idan aka cigaba da biyan kuɗin digital a kasashen Afirka renon Faransa, zai shafi kasancewar harshen Faransanci a internet cikin kankanin lokaci.

[22] A shekara 2018, ƙirar ta ɗauki matakin yawan harsuna da yawa kusan 25%, da sakamakon yaren farko da na biyu (L1+L2) don haka aka kafa, a matsayin kashi, bisa 125% don yin la'akari da yawan harsuna. A cikin wannan sabon sashe na 2022, saboda haka, bayanan Ethnologie, ma'aunin harsuna da yawa ya karu zuwa 43%.

[23] A kan harsuna 329 tare da masu magana da harshen suna sama da miliyan ɗaya.

**MA'NAR MANUNAI DA AKA SAMAR DUKA IRI ƊAYA NE, AN RIƘE (MAI KARFIN) WANDA YA DACE DA AWON MANUNAI GUDA SHIDA:**

**MAI AMFANI DA WEB** = Yawan masu Magana da harshe 'yan asali (da aka samu nauyin hada data na kasashe da kuma datar wurin harsuna)

**YAWAN MASU AMFANI DA WEB** = Yawan masu amfani da web na duniya (yawan masu amfani da aka samu da ya nuna kashin na kowace kasa)

**AMFANI** = Yawan harshe da ake da shia hanyoyi da yadda ake aiki da shi (misali, yawan hanyoyin hulda da masu amfani da hanyoyin sadarwa)

**JERIN KASASHE** = Sayin kasashe bias yadda aka jera su ta manunin baya nin al'umma (misali ingancin gwamnatin-e da yawan kowane harshe)

**ABUBUWAN DAKE CIKI** = Yawan shafukan gama-duniya na web

**YADDA AKE HADA SU** = Girman yadda ake hadasu kamar hada harshe da hanyoyin ko harshen fassara a wajen sadarwa

Wannan manuni ya tattaro duk martabar da kasancewar harshen a internet.

Duk martabobi (gyararrun kura-kurai a madogara) waɗanda aka samo daga samfuri sun ba da waɗannan rabe-rabe.

| DARAJA | LANHARSHE | HALLARA |
|---|---|---|
| 1 | Ingilishi | 25,00 % |
| 2 | ***Sinanci*** | 15,00 % |
| 3 | Ispanianci | 7,00 % |
| 4 | Faranasanci | 3,50 % |
| 4 | Harshen Hindi | 3,50 % |
| 6 | Harshen Portugal | 3,00 % |
| 6 | Harshen Rasha | 3,00 % |
| 8 | ***Larabci*** | 2,50 % |
| 8 | Jamusanci | 2,50 % |
| 8 | Harshen Japan | 2,50 % |
| 11 | ***Harshen Malayshiya*** | 1,80 % |
| 12 | Italiyanci | 1,40 % |
| 13 | Harshen Turkiya | 1,20 % |
| 14 | Harshen Korea | 1,20 % |
| 15 | Harshen Bengali | 1,20 % |
| | **SAURANSU** | **25,70 %** |

### Amfanin harshen faransanci a hayoyin sadarwa digital

Muhimman hanyoyi guda biyu dake nuna harshen Faransanci a sadarwa digital su ne:

1. **Rahoto (L1 + L2)/ L1**, mai numa yawan yadda ake amfani da harshe a matsayin harshen a na biyu, in da Faransanci shi ne na biyar.
2. **Yawan ƙasashe in da ake da masu magana da harshe**, a nan Faransanci shi ne na biyu bayan Ingilishi[24].

Wannan ya sa za a cika sabon manuni a: **ga yawan yaɗuwar harshe a duniya (DML)**. An bayyana shi kamar haka: DML= (L1 + L2), L2 x percentage na kasashe da ake magana da harshen.

Sabon manuni ya ba da damar a raba ƙasashe ta hanyar haɗa tsari biyu dake nuni da yanayin ƙasa da yawan jama'ar da ke wurin da harshe yake: wannan haka yaba da wata kima da za a juya ta zuwa wani kasha a tsari da bambanci. Shi DML, a tsarance shi ke nuna halin da harshe ke ciki a cyberspace (wato a fagen cyber).

Harsunan da aka ba da rahotunsu (L1 + L2)/L1 da ma'aunin da yafi 2.5 suna kan tsari kamar haka: Dioula, da Swahili da Ingilishi da Bamanakan fa Faransanci da Ourdou da Malais da Sotho ta Arewa da Thailandese. Kuma harsunan da ake magana da su a fiye da kasashe 35 su ne: Ingilishi da Faransanci da Ispaniyanci da Larabci.

Ta fannin ninka yawan kimar harshe a faɗin duniya (DML) ta duba yawan masu magana da harshe, wannan yana nuna **matsayin yaɗuwar cyber a duniya (DCL)** da ta harshe (DCL – DML x % Conn), manuni ne dake taƙaita karfin harsuna dake bazuwa a duniya ta sadarwa digital. Idan aka kara da yadda ake shiga internet kimar DCL ita ke gyara DML in an yi la'akari da matsayin kowane harshe a internet.

Yawan da aka karkasa, shi ke ba mu damar aunawa da kuma ganin irin tazarar da ke nuna harshen Ingilishi da Faransanci suke kan gaba fiye da sauran harsuna, bisa tsarin dake nuna yadda aka shirya da kowane harshe a tsarin game-duniya (DML) da kuma shirin amfani da harsuna masu yaawa da ake yi a internet (DCL). Adadin kimar shi ke nuna rabon manuni guda biyu da ya shafi duka harsunan da aka yi la'akari da su kamar haka: Ingilishi da Faransanci suna da kashi 25% na rabon da babbar tazara a gaban harshen Jamus da Rashea da Ispaniyanci, sannan sai Larabci da Malay da Italiyanci da Sinanci.

[24] Ƙididdigar da aka yi don harsuna 329 na fiye da masu magana da miliyan ɗaya L1, tare da data na yanan gizo a Satumba 2021 kuma dangane da ƙasashe (ko yankuna) 215 da aka zaɓa a cikin ƙirar.

| HARSHE | DML | DML% | DCL | DCL% |
|---|---|---|---|---|
| ***Ingilishi*** | 2,51 | 12,68 % | 1,61 | 14,24 % |
| ***Faransanci*** | 1,69 | 8,52 % | 1,09 | 9,66 % |
| ***Jamusanci*** | 0,48 | 2,45 % | 0,42 | 3,75 % |
| ***Harshen Rasha*** | 0,40 | 2,01 % | 0,31 | 2,76 % |
| ***Ispaniyanci*** | 0,37 | 1,90 % | 0,27 | 2,40 % |
| ***Larabci*** | 0,30 | 1,51 % | 0,18 | 1,56 % |
| ***Harshen Malayshiya*** | 0,33 | 1,69 % | 0,17 | 1,51 % |
| Italiyanci | 0,22 | 1,13 % | 0,17 | 1,50 % |
| ***Sinanci*** | 0,25 | 1,27 % | 0,16 | 1,46 % |

### Matsayin sauran harsuna

Harsunan da ake amfani da su a internet in aka cire son zuciya (in aka kwatanta da yawan Faransanci wanda yake da kashi 65.5%) su ne:

| Harsuna | Adadi masu magana Masu magana ta yanar gizo |
|---|---|
| Harshen Norway | 97,87 % |
| Harshen Denmark | 97,83 % |
| Harshen Sweden | 93,49 % |
| Harshen Japan | 92,62 % |
| Harshen Holland | 92,02 % |
| Harshen Luxembourg | 91,90 % |
| Harhen Switzerland da Jamus | 91,56 % |
| Harshen Catalan | 90,50 % |
| Harshen Flamand ta Yamma | 90,43 % |

### Matsayin ingilishi

Matsayin Ingilishi yana ta samun koma-baya ne daga kashi 30% a shekara ta 2017 sai ya dawo kashi 25% a shekara ta 2021; sai dai kafofin sadarwa suna bayanin son zuciya saboda rashin la'akari da amfani da harsuna da yawa, suna bayyana kashi fiye da 50%. Gaskiyar magana ita ce, an sami sauyi sosai a sadarwar internet a shekara goma da suka wuce saboda tururuwar masu sadarwa a internet da harsunan Asiya da kuma Larabci. Yawan masu amfani da Ingilishi kuwa na (L1+L2) kamar yadda masu kula da harsuna da al'adu mabambanta a internet suka kiyasta ya kai kashi 32% a shekara ta 2007, sai dai a halin da ake ciki ya dawo kashi 15%.

## AL'ADUN MUTANAE MASU MAGANA DA HARSHEN FARANSANCI DA KE ZUBE A YANAR GIZOI: ABUBUWAN DA SUKA SHAFE SU DA KUMA MATSALOLINSU

Duk da muhimmancin al'ada da ayyukan fasaha mabambanta da ake bayyanawa a ƙasashe renon- Faransa, ba a ciki samun su a kafar yanar-gizo ba[25]. Tsarin da ake bi na sa wa da raba al'adun ya rikita nema da samarwa musamman don ya amfani GAFAM[26]. Masu juya wannan kafar sadarwa ta game-duniya suna amfani da fasahar ci gaba wajen raba al'adar yadda suka ga dama, wanda hakan ke barazana ga fito da al'adun kasashen renon Faransa.

### ■ Muhimman abubuwan al'da da ƙirƙira[27]

CCI, yau suna ba da babbar gudunmuwa a duniya ta fuskar ɗaukan aiki da tattallin arziki. Canjin da suka kawo a sadarwa ta digital ta shafi ƙasashe duka sannan suna tafiya tare da ci-gaban fasaha da canjin kafofin sadarwa ga jama'a. Duk da bambance-bambancen yankuna, mafi yawan jama'ar yanzu suna amfani da hanyoyin sadarwar digital, su shiga CCI.

Silma da kiɗa da rawa da waƙa da ake kallo suna ta komowa hanyar sadarwa ta digital tun shekaru masu yawa. Fitattun 'yan fim na duniya tuni suka shirya tsaf suna ta cin kasuwar kwashe masu kallo da yawa.

Ta ɓangaren ƙasashe renon-Faransa, ana ta fitar da shiryeshirye iri-iri na (TV5MONDEplus da aka ƙaddamar a watan Satumba na shekara ta 2022, da kuma le Fonds Francophonie TV5MONDE plus wanda aka ƙaddamar a watan Maris na shekara ta 2021), ko kuma sun daɗe suna wanzuwa tun shekaru masu yawa (le fonds/image de la Francophonie).

[25] Yanayin wasan ganowa da samun damar yin amfani da abun cikin al'adun Faransanci akan Intanet, 2020. Duba qrcode.
[26] Taƙaitaccen suna da a ka ƙirƙiro daga sunayen manyan rukunai: Google, Amazon, Facebook, Apple, Microsoft, da sauransu, wadanda za a iya karawa da Spotify, Deezer, da sauransu.
[27] A al'adu da m masana'antu a duniya a cikin dijital zamani, Bincike da za'ayi domin OIF da Post-Advisors suka yi, Juin 2021. Duba qrcode.

### MENENE ABIN GANOWA?

**Wannan sabon ra'ayi, wanda aka ƙirƙira kuma ya haɓaka tun 2016 daga Kanada, yana bayyana tsarin gamuwa tsakanin abun ciki da jama'a a cikin yanayin digital :**

**■ Ainihin siffa ta kowane abun ciki da ke kan yanan gizo don zama mai iya ganewa cikin sauki kuma mai amfani wanda zai samu bukatu akan injunan bincike;**

**■ Girman da ba zato ba tsammani na gano abun ciki wanda mutum baya tsammani da/ko wanda bai sa da shi ba;**

**■ Shawarar abun ciki na al'adu ba tare da bukatar mai amfani ba;**

**Ganowa don haka ya ƙunshi abubuwan al'adu na buƙatu :**

**■ ganowa (nassoshi da index);**


**■ samuwa (ci gaba da samar da isasshen tayin : shawarwari (haɓaka ganuwa).**

### ■ Fasahar hanyoyin tsari da aka gano

Fitowar tsararre yanan gizo 3.0 kuma daidaitacen komfutata yadda za a karanta bayani, yau, ya sa hanyar sadarwa tana tsarawa kuma tana raba bayanai da za a sake amfani da su a bayyane. Abubuwa biyu suka dace da abin da aka gano na sadarwar zamani. Da ta da hanyar samar da yaki, kowane kashi yana da na shi bambanci lissafi a zuciyar tsarin ba da shawara.

Na'urar da za ta iya raba data (ta rarraba) a tsakanin hanyoyin guda biyu yana da muhimmanci ga abin da ke samar da al'ada a cikin hanyoyin sadarwa zamani.

### Adadin masu amfani da yanan gizo a Duniya




**53,6 %** cna mutanen Duniya suna amfani da yanar gizo a 2017.

**47 %** a kasashe masu tasowa.

**19,1 %** matalautan kasashe.

Tushe : ***Les Industries culturelles et créatives dans le monde à l'heure du numérique,*** étude Post Advisors, juin 2021

### Babban fanni na tattalin arzikin duniya

**$ 2,250 billion**
gudunmawar shekara-shekara na masana'antun ƙere ƙere ga GDP na duniya dadai da 2.6%


Gurbin aiki **miliyan 30**
a ma'aunin duniya, ciki har da na yau da kullun.

**20 % na matasa**
20 % na ma'aikata a sashen CCI suna tsakanin shekaru 15 zuwa 29..

**45 % na mata**
45 % na ma''aikata CCI mata ne

Tushe : ***Les Industries culturelles et créatives dans le monde à l'heure du numérique,*** étude Post Advisors, juin 2021

### Adadin streaming na vidéo da kide




**62%** na amfani da dijital na duniya na jerin asali **Netflix**. (OIF, 2020)


**345 miliyan** masu amfani aiki kowane wata a Spotfy 2021 (**Les Echos**)

Ana dora sa'o'i 500 na bidiyokowane minti ɗaya (***Statistica***)

Streaming na video yana da kashi 61% n na zirga-zirgar intanet na duniya (***Statistica***)

Tushe : ***Les Industries culturelles et créatives dans le monde à l'heure du numérique,*** étude Post Advisors, juin 2021

### Aakaluma Kalubalen ganowa




ABUN GANOWA
40% na tallacetallacen littattafai a kan Amazon sun fito ne daga injin bincikensa

SAMUWA
26% na abun ciki da ake samu akan sabis na bidiyo akan bukata a cikin Tarayyar na Turai ne. (OIF, 2020)

SHAWARA
60% na abubuwan da aka gani akan Netflix shine sakamakon shawarwarin da aka samu daga dandamal


Tushe : ***Les Industries culturelles et créatives dans le monde à l'heure du numérique,*** étude Post Advisors, juin 2021

**■ Abin da aka gano da ikon ƙasa da masu ruwa-da-tsaki**


Hatsarin daidaita amfani da al’ada da ƙarancin samun tattalin arziki don ci-gaba kowace al’umma yanzu suna da muhimmanci.

Abin da aka gano ya ƙunshi abubuwa da suke da nasaba da ikon ƙasashe: kamar adana al’adun jama’a da tallafawa da kuma shiga kasuwannin duniya da na ƙasa domin nuna al’adu a hanyar sadarwa digital; da ƙarfin da ‘yan fim na ƙasa suke da shi wajen aiwatar da isasshen tsarin hanyoyin gudanarwa. Tsarin digital ƙasashe renon-Faransa daga shekara ta 2022 zuwa 2026 wanda ƙasashen suka amince da shi a watan Disamba na shekara ta 2021[28]. Ya yi la’akari ire-iren ƙalubalen da za a fuskanta.

Kasashe-renon-Faransa da gwamnatocinsu, da masana’antu, da masu zaman kansu da jaruman fim da jaruman ƙungiyoyin farar hula da ƙungiyoyi na ƙasa da ƙasa duk suna da ruwa-da-tsaki da abin da aka gano.



Tushe : ***Pour une initiative francophone en faveur de la découvrabilité en ligne des contenus francophone***, OIF




## LITTAFIN DA KUMA MAWALLAFAN HARSHEN FARANSANCI

Ba sai an tambaya ba rubutu shi ne hanya fitacciya na bunƙasa al’adun magana da Faransanci mabambanta. Shi ne kuma zuciyar da take ƙirƙira da ƙagowa da ƙarfafa harshen Faransanci. Littafi a kowace irin sifa yake har da na digital, an buga shi ne daga sanin tarihin al’ada. A ƙarƙashin waɗannan fannoni guda biyu wato: al’ada da tattalin arziki, an lura tun-tuni, suka bayyana saɓanin ra’ayi wani lokaci mai tada hankali sai kuma dai yana ƙunshe da arziki da alƙawura.

**■ Taron da aka yi a kan matsayin littafi a duniya**

Taron matsayin littafi a duniya an yi shi ne a ranar 23 zuwa 24 watan Satumba na shekara ta 2021 a birnin Tunis. Mahalarta taron (da suka je ko a ka gansu ta hanyar sadarwa) sun fi mutum ɗari huɗu; marubuta da jarumai da shugabannin cibiyoyi ilimi da na ƙungiyoyin siyasa daga ko’ina da ake magana da Faransanci a duniya. Kasashe da gwamnatocin da suka shirya taron su ne: (Cote d’Ivoire, da Republic of Guinea da Quebec da Swiss Confederation da Tunisia da the Wallonia Brussel Federal). Har da ƙungiyar duniya ta masu magana da Faransanci. Taron ya haɗa masu ruwa-da-tsaki a harkar littafi guda dubu daga ƙasashe arba’in da biyar. An fitar da batutuwa muhimmai guda goma da za a aiwatar (daga cikin guda 50[29] da aka gabatar)

Game da waɗannan shawarwari an ba da misali da ƙasashe guda tara[30]. An cim ma matsaya ta musamman dangane da al’ada da ilimi da ya shafi ƙasashen da gwamnatocinsu domin a tallata littattafai a kuma bunƙasa karatu da kuma tallafawa masu ƙirƙira, da aikin fassara zuwa Faransanci da yaɗa waɗannan ayyukan da mawallafa da kuma ƙarfafa manufar ɗakunan karatu.

Kafin a yi babban taro bincike masu yawa sun sa an gano halayen sharhi da ake yi da Faransanci da matsayinsu a kasuwa da kuma yadda za a bunƙasa su; akwai ra’ayoyi guda bakwai[31] na sharhin Faransanci da kasuwancinsa da ofishin wallafa da Faransanci na duniya ya ƙirƙiro (BIEF) da nazarin da Bearing Point, suka yi mai suna: “Littafin harshen Faransanci a shekara ta 2020 da kuma 2050[32]”

Sakamakon waɗannan bincike ya ba mahalarta taron duniya damar jaddada matsaya a kan batutuwa kamar haka: Samun tsarin shari’a, damar zagawa da kayan aiki da kuma littafai da inganta dangantaka da sadarwa a tsakanin ƙwararru. Ta fuskar sadarwar nan, abin da aka sa a gaba shi ne samar da sadarwar digital ta ruwa-da-tsaki na littafin harshen Faransanci[33] na OIF. Wannan dama ce da za ta sa a nemi shirye-shiryen da OIF ya yi da zai shafi duk wani mataki na tsara littafin kamar: ƙirƙira da bugawa da rabawa da tallatawa. Sanna a daɗa bayyana goyon bayan tsare-tsaren don mutane su karanta a ƙasashe ta hanyar sadarwa (CLAC) a cibiyoyin karatu da al’ada waɗanda suke ƙasashe ashirin na kuɗu; da kuma ba da kyauta ga yankuna guda biyar na LA Francophone, a matsayin kyauta ga marubuci mai magana da Faransanci a duk shekara, da za ta ba shi damar zuwa “yawon-buɗe-idon-adabi” a faɗin duniya.

**■ Taron marubuta da harshen Faransanci**

An ƙirƙiro shi a shekara ta 2019; waɗanda suka ƙirƙiro su ne Leila Slimani da Marigariya Michel le Brios. An yi taron marubuta da harshen Faransanci na duniya a birnin Tunis, ranar 25 zuwa 2 6 ga watan Satumba, na shekara ta 2021 da taimakon OIF da wasu ‘Yan kwamitin marubuta su ne asali wanda ya ƙunshi: Leila Slimani da Fawzai Zouari da Lauren Gaude da Yanick Lahens da Felwine Sarr har zuwa watan Janairu na shekara ta 2021. Marubuta kusan talatin daga ƙasashe biyar suka sami halarttar taron ko suka shigo ta hanyar sadarwa zamani; an tattauna a matsayin wata kafa ta ganawa da gudanar da taro da masayar ra’ayi.

[29] Pour une nouvelle dynamique du livre en langue française dans le monde : Cahier de propositions et 10 recommandations prioritaires, 2021.
Duba qrcode.

[30] Burkina Faso, Côte d’Ivoire, Faransa, Madagascar, Québec, Switzerland, Tunisiya, Vietnam da Tarayyar Wallonie-Bruxelles

[31] Duba qrcode.

[32] Le livre en langue française en 2030 et 2050, Étude économique prospective, Bearing Point. Duba qrcode.

[33] Duba qrcode.

## Rahoton l'OIF
## Harshen Faransanci a Duniya 2022

**Mai Gudanarwa :** Nivine Khaled, Daraktan Harshen Faransanci da Bambance-bambancen Al'adu na Faransanci (DLC).

**Babban mai Shiryawa da Rubutawa :** Alexandre Wolff, Manajan Observatoire de la langue française.

**Shiryawa da Rubutawa :** Francine Quéméner, Kwarariyar Shirrin Observatoire de la langue française (enseignement du / en français) et les politiques linguistiques.

**Rubutawa (DLC) :** Véronique Girard, Kwararriyar Dhirrin (découvrabilité des contenus culturels) ; Aurélia Grosu, Mai bada umurni (langue française et multilinguisme dans les OI).

**Masu taimakawa :** Mirana Andrianasy (stagiaire) ; Pauline Hardouin (assistante de programme pour l'Observatoire de la langue française).

**Masu ba da gudumawa :** Bernard Cerquiglini, Souleymane Bachir Diagne, Jean-Marie Klinkenberg, Richard Marcoux, Florence Mourlhon Dallies, Daniel Pimienta, Laurent Richard, Destiny Tchehouali, Rada Tirvassen.

Wannan aiki tsaru ne na littafi
***Harshen Faransanci a Duniya 2022***
Wanda zai fito Bugun Gallimard a Watan Maris 2022

© Éditions Gallimard, 2022.